Duk da irin saurin da nake yi bai hana na tsaya na jira shi ya fito ba. Kasancewar ina girmama dukkan abin da ya sha fe shi.   Kusan rabin awa kafin ya fito.
K'afafun sa da ya zuro na zubawa idanu ina kallo, yadda halittar k'afar ta cika kai ka ce shi ne ya zana abarsa.
Bayan haske da k'afar take da shi ta kasan ce tana wani irin walwali mai d'auk'ar idanu.  Duk da hannu bai tab'a ba tabbas ma'abocin kallonta ya san fatar zata yi laushi.  Shadda ce sanye a jikinsa mai launin ruwan toka.

Haka hular kansa take ita ma. Fuskarsa kuwa sai walwali take kamar hasken wata daran goma sha biyar. Sajen fuskar kuwa kai ka ce wani mai ya kwaranya a wurin yadda yake shek'i da walwali.

Amma duk da wannan yanayi na fuskar sa bai sa ya cika cif ba, saboda kowacce halitta cikar kyaunta tana k'ara cika a lokacin da fuskar ta kasance cikin murmushi.

Kallon gatsali na yi masa cike da jin haushin sa yadda yake jin kansa kamar wani na mijin kirki. A zahiri kuwa cewa na yi; ''Sannu da fitowa bombino."

Halin na sa ya yi mini wanda ya sa ba, wato k'in amsa magana a kan lokacin ta.  Sai chan sannan ya bud'e karamin bakin sa ya ce dani.  "Yawwa, muje na sauk'e ki a school tunda ba ki fita ba."

"Idan ka kaini kuma da wacce mota zan dawo? Ai gwanda na je da motata."  Na furta cikin sakin fuska .   Bai kalle ni  ba ya fara shirin fita daga falon sai da na mik'e ina bin sa sannan yace; "Wanda ya kaiki ai zai iya d'auko ki."
Ban tanka masa ba na wuce na je na shiga motarsa ya shiga shi ma ya ja muka fita mai gadi ya rufe k'ofa.

Tafiyar kurame mukeyi ni da shi ba wanda ya kuma yiwa d'an uwansa magana.  Daidai bakin makarantar mu ya ajjiye ni  wacce take anguwar ta'alawa a cikin garin gaidam.  Ha'islamic ita ce makarantar da nake zuwa karatun addini duk ranar asabar da lahadi.   Ina fitowa kuwa idanuna cikin na nabila k'awata da maryam sun kusa k'arasowa bakin get d'in makarantar.
Murmushi na sakar masu na kulle masa motar sa ya ja ya tafi.    K'arasowa sukayi muka gaisa suna ta min tsiya da matar mijin ta, sunan da suke k'irana da shi ke nan.

Ban ce da su uffan ba na wuce suka rufa min baya.Muna shiga muka hangi malamin tauhidin mu ya shiga ajinmu.  Da sauri muka k'arasa dukanmu muka shiga ajin.   Karatu ya mana sannan ya d'aura da mana nasiha ya fita.

Yana fita kuwa adama me dambun kifi ta wangale bakin robar dambu da nufin mu siya. Jujjuya shi na yi na dubi k'awayena na ce da su kowa ya d'au d'aurin naira d'ari-d'ari zan ba ta kud'in.
Ko da jin haka tuni adama ta yarfa tafi tare da fad'in; " Ahayye! Ka ga manyan mata masu aji

sun bayar da yawa an cika masu aljihu."   Idanu na zaro sosai nace; " Adama, muna cikin islamiyya kike cewa haka?"

" Yo mene ne a ciki tunda dai gaskiya na fad'a, ke ni wallahi kina burgeni irin yadda mijin ki yake ji dake d'innan."  Adama ta fad'a tana kaimin dukan wasa kan cinyata.

Gab'a d'aya sai kunya ta lullub'eni na sunkuyar da kai k'asa, cikin zuciyata kuwa ji na yi wani irin d'aci ya mamaye min ita sanadin yadda kowa yake min kallon macen da take more rayuwa a gidan bombino.   Da sun san irin tashin hankalin da nake ciki da ba za su ce haka ba. Su kuwa su nabila tuni kowa ya washe baki suka d'auki na su d'aurin suna sha suna saka min albarka tare da cewa adama; "Wallahi ke dai kin shiga uku da shegen b'aran-b'aramarki, sai kinje wataran kin manta kinyi a gaban malam tukunna."

"Ke rufa mun asiri! Da ranar na fita ta taga kuwa. Yadda malam yake min kallon nutsatstsa." Adama ta fad'a tana rik'e haba.

Kafin su kai ga bata amsa malamin da yake mana tafsiri na alku'rani ya shigo. Don haka tuni muka nutsu muka gyara zama .

Misalin k'arfe shabiyu na rana aka mana fatiha muka fito muna hirarakin mu wanda muka saba yi na raha da juna.

Kamar an ce na d'aga idanuna na kalli bishiyar da take k'ofar makarantar na hango shi zaune cikin motar sa yana latsa wayarsa.

Maryam tace; "To Samha anan zamu rabe ga chan mijinki ya zo d'aukar ki don haka ba ni littafina na tafsiri mayi magana ta wasaf."   "Ke kam ki barmin mana na je na duba sosai tunda na wa ya b'ace k'asa ko sama." Na fad'i haka ina marairaice fuska."Kayya sa! Ai kawai ba ni abina kiyi hak'uri saboda kanki ya fi nawa ja kin sani sosai."

Sanin halin bombino zai iya juya motar sa ya tafi idan na tsaya b'ata lokaci tuni na b'ata kayanta na na wuce ina murgud'a mata baki ina harararta     Na ce; "Sannu me kan dankali."

Ko da na shiga cikin motar da sallama na shiga ina kallon yadda yake danna wayar sa cikin nutsuwa, amma kuma bai ko waiwayo ya dube ni ba bare ya amsa min.  Wani k'arago me tauri na ji ya tsaya min cikin mak'ogwarona ga wasu kwallah da suka cikamin idanu kasancewa ta mai saurin kuka.

Jin ya tayar da motar shine ya tabbatar min da cewa lalle ba zai tanka min sallamar ba.   Ba wata tafiya me nisa mukayi ba muka zo gida da yake muna anguwar laa'anti da zama

Bayan me gadi ya bude mana mun shiga har zai wuce na ce; "Yanzu Awwal halinka na yiwa mutun banza har ya kai ka fara k'in amsa sallama?"

"Au daman ce miki a kayi dole sai an amsa sallama a zahiri tukunna kake da ladan?"  Ya ba ni amsa.

Ban ce komai ba na wuce d'akina na cire kayan makarantar da yake jikina.

Tunanin abin da zan dafa mana nake kasancewar yaran nawa suna gidan hajiya mahaifiyarsa, chan duk ranar juma'a suke tafiya sai lahadi za su dawo da yamma saboda makaranta. Ganin zaman tunanin zai sa na b'ata lokaci sai kawaina wuce madafa na dora jalof d'in taliya wacce ta ji kayan miya da bushashshen kifi .

Kunun aya na had'a mai rai da lafiya ta ke na gama komai kasancewar na yi amfani da gas

ne. Kan daining table na shirya komai .

Ganin Awwal zaune kan d'aya daga cikin kujerun falon  yana murmushi sai na ji farin ciki ya kamani . Da yake ba ni da zuciya wajen biyan bukatar zuciyata kuma ganin yara basa gida na ce bari na yi amfani da damata.

Cikin sauri na shiga toilet na fesa wanka na kwara turaren wanka mai k'amshin gaske a jikina na fito na saka kaya masu kyua riga da wando wanda ko mak'iya su ka kalla tabbas ya san na yi kyau kayan sun zauna min daram.  Mai me kamshi na shafa na saka hoda da lipstic na sanya wata hula kalar kayan na sake feshe jikina da turare masu kamshi.

Da yake na yi alwala daman, sallaya na d'auka da hijabina na fita falo domin muyi jam'i idan a gida zayyi.

Ina fita kuwa na tarar ya shimfid'a sallaya ya kalli gabas yana shirin tayar da ikamar sallah, bayan sa na shimfid'a na bisa mukayi sallah har muka sallame.   Bayan addu'o'i sannan na ta shi na lunke hijabina na ajje kan hannun kujera tare da sallayar na gifta ta gabansa ina wani irin taku wanda dukkan wani mai lafiya idan akayi masa haka tabbas na san zai ji a cikin jikin sa.

Tun kafin na ida zama na ke jiyo takunsa ya nufo ni zuwa wurin daining table d'in. Har wani runtse idanuna nake yi ina jin yau de kam na gama da shi tabbas na san hak'ata zata cimma ruwa.

Jin shiru shine ya ba ni damar bude idanuna na hamgoshi yana gyara labulen wurin.   Duk sai na ji jikina yayi sanyi sosai .  Abinc na zuba masa na zuba nawa na saka mana cokali na zauna tare da fad'in bismillah. Wuri ya samu ya zauna ya kalle ni da halamun murmushi ya ce, "Sannu da hidima."  Har cikin zuciyata na ji dadin yabon duk da cewa ba yau ya fara ba, saboda abin ya zame masa kamar sabo ko na ce sara.

Har muka gama cin abincin ina satar kallon sa ina kallon yadda idanun sa suka sauya kala zuwa launin ja a maimakon farare kuma yana lumshe min su da wani irin kallo wanda na tabbatarwa da kaina tabbas hak'ata zata cimma ruwa.

Sai dai kash! Yana gama cin abincin ya mike ya wuce falo ya kwanta kan kujera yana ta zabga hamma . Ko da na gyara wurin na zauna gefen sa naga yadda zamu kaya na d'auki rimot na tv na kama tasha sai ji nayi ya ce, "Don Allah Samha bacci zanyi kije falon ki kiyi kallon mana."

Wata mahngurbar damuwa ta ziyarci ziciyata kamar na zuga masa zagi na mik'e a fusace na ce;  "Ko baka fad'a ba tabbas zanyi hakan!" Har ina had'a hanya na wuce uwar d'aka na fad'a gadona tare da barkewa da kuka.

Me Awwal yake nufi da ni ne? Ba shi da ishashiyar lafiya ne ko kuwa dai ina da matslane wacce za ta hana shi ya sauke hakkin da yake kansa? Wace rayuwa ce hakan? Kullum a ce miji yana guduna sai rabon haihu ya zo sannan zamu zam abu guda? Idan har ba ni da lafiya ko ina da matsala tabbas ya kamata na ga haka a lokacin da k'addarar haihuwa ta kawo shi wurina. Idan kuwa haka ne Awwal shi ne da matsala ba ni ba, to amma ta ya zan iya magance wannan matsalar cikin sauki? Idan na ce zan rabu da Awwal kan wannan dalilin to ta wacce siffa zan bayyanawa iyayen nawa matsalar? Saboda magana ce me girma. Haka zalika yadda 'yan uwa da dangi da sauran mutane suke ji cewa na fi kowacce mace sa'ar samun miji na gari da kulawa ba zasu gamsu da magana ta ba.

Musamman idan aka duba yadda Awwal yake da k'ira da karfi da kwarjini ga yanayin idanun

sa sak na kwaratan da suka kware wajen kallon matan mutane a titi. Duk da cewa na shi idanun kalar su ce haka. To don haka zayyi wuya abin da zan fad'a ya zauna akan al'umma.Kuma idan har na ce zan bar Awwal na barshi ba tare da d'aukar wani mataki ba tabbas rayuwata tana cikin hatsari. Domin d'ayan biyu ne.

Ko na tabbata cikin b'akin ciki ko kuma na zama mage da wuri. Da irin wad'annan tunanin bacci yayi gaba da ni.

Ban farka ba sai kusan hud'u saura.

Don haka alawala na shiga toilet na yi na tayar da sallah ba tare da na fita falo ba. Bayan na idar ne na fita domin na je kitchen na d'aura girkin dare.

Yadda na barshi yana baccin asara haka na tarar da shi. Har zan tayar da shi sallah a zuciyata na ce barshi shi ya sani yayi ta baccin tunda shi ne ya koreni.

Ina chan ina aiki na ji motsin yana sallah a falo. Dan haka da na fito falo na zauna ina jira abin da na d'aura ya nuna, har ya idar da sallah ya dube ni.

"Wai daman kin farka amma baki tayar
dani na yi sallah ba? Ya ce da ni.

"Kai fa ka ce na barka kayi bacci, tunda baccin ya fi komai mahimmanci a rayuwarka me zai sa na ta she ka daga bacci?" Na bashi amsa cikin fusata.

Kallona ya yi ya kauda kai sannan ya ce. "Lokuta da dama kina fad'amin kalamai marasa d'adi ina hak'ura amma abin ya fara isa ta fa."

"Au iya kalamai ne ma? Ai da sauki tunda ba cutarwa!" Na ba shi amsa na wuce kitchen

Shuru ya yi yana nazarin, chan kuma sai ya mik'e yana fad'in; "Yau zan kawo k'arshen rainin nan naki Samha!"

Ya fad'a da k'arfi ta yadda zan iya jiyowa....

2

"Hummm! Ka yi ka gama wallahi indai baka sauya haliba kad'anne ka gani."
Na furta ta yadda ba zai jiyo ba. Aikina na saka a gaba har na kammala na gyara ko ina ina faman had'a gumi, don haka falo na koma na zauna ina shan ac har na huce. Ana shirin yin sallah na shiga toilet na watsa ruwa tare da alwala na fito na saka wata doguwar riga mara nauyi ta yadda ba zanji zafi ya takuramin ba ko da an d'auke wuta, tunda sai ya ga dama zai kunna mana inji yau kam yana ji da bala'i.

Bayan na yi sallah ina zaune ina lazumi ban ji motsin shi ba hakan ya tabbatar min da baya gidan tun da mukayi magana sanda nake kitchen, kan kujera na koma na zauna ina jiran na ji da me zai dawo amma shuru. Sai kawai na mance da batun sa bayan na yi sallar isha na hau online muka fara bitar karatun mu da k'awayena na school.

Jin shigowar motar sa ce ta sa na kashe datar domin na ga zuwan sa.

Hankalina na maida kan tv ina kallo sai na ji ya yi sallama, ina juyawa tare da amsawa na ga kawu habu k'anin mahaifiyata ya rufa masa baya suna shigowa.

Cikin zuciyata na ayyana ke nan k'arata ya kai.

Zamowa na yi daga kan kujerar ina fad'in; "Kawu barka da zuwa, kaine a tafe ke nan?"

Wani kallo ya watsamin tare da fad'in, "kin ci gidan ku Samhatu! Kinji ko, wato ke da muke ganin kin fi kowa hankali cikin 'yan uwanki ashe ba haka bane. Yanzu Samhatu mene ne kika rasa a gidan yaron nan Awwalu, kin samu ci sha sutura walwa kina makaranta, yaron nan har da mota ya siya miki, duk fad'in garin ku mata na wa ne kuke da mota? Ke baki ga wannan ma darajawa ba ce. Alheri kuwa kaf! Family kowa ya san da shi. Yaran ki duka sun banbanta da na sauran mutane, wajen sutura da walwala. Ku ci me kyau ku sha me kyau akwai abin da kike nema fiye da hakan"

Wallahi ki shiga hankalinki, kiyi wa mijinki biyayya karna kuma jin ya kawo kashenki."

Lumfasawa na yi tare da juyawa na kalli shi me kai k'arar sai na ga wayam ba shi ba labarinsa ashe ya wuce d'akinsa. Cike da damuwa na ce; "Kawu ka yi hakuri zan kiyaye hakan in sha Allah."

"Yawwa da dai ya fi miki dai a wannan zamanin zaman auren shine rufin asirinki."

Ya fad'a tare da juyawa zai fita a falon daman ko zama bayyi ba. Awwal ne ya fito ya bi bayan sa yana fad'in Kawu bari ma maida kai gida .

Fita suka yi na koma falo na zauna gajaf a kan kujerar na ce, "Zaman aure ko zaman girki?" Sanin ba ni da amsa shine ya sakani na bud'e data na cigaba da karatuna.

Kusan goma na dare sannan ya dawo, abinci na je na zuba masa na ajjiye a gabansa nima na zuba nawa. Da bismillah muka fara ci, can sai na dube shi na ce, "Ka kai k'arata wurin Kawu maimakon ka zauna da ni ka tambayeni dalilin faruwar hakan. Ko da yake kasan amsar kawai rashin girmama auren ne da kuma rashin soyayya."

Har muka kammala cin abincin bai kulani ba sai da ya zo tafiya ya ce dani, "Ina jiranki a d'akina, kuma karki wuce shad'aya baki zoba."

Yana gama fad'ar haka ya fice abin sa zuwa d'akinsa.

Da sassarfa na bi hanyar d'akina ina ganin duhu-duhu saboda zallar damuwar da nake ji a zuciyata, anya kuwa Awwal ba zai saka min hawan jini ba? Yanzu wannan wacce irin rayuwa ce haka? Hummm! Allah ka shiga lamarina. Na furta a cikin zuciyata.

Shirya kaina na yi cikin shiri na musamman, ina addu'a araina Allah ya sa na yi kwanan farin ciki.

Ko da na tura k'ofa yana kwance ya juya min baya wanda hakan kusan ya zame masa sabo. Ko kunyata ma yake ji ban sani ba, domin kuwa Awwal matukar ya zo da wata b'ukata to mungama had'e idanu da shi sai kuma yinin ranar wajajen yamma. Ni fatana Allah ya sa ba rabon wani cikine ya kawoni yau ba, saboda a yanzu a halin da nake ciki mafita ya kamata na nema ba wai na cigaba da haihuwa da shi a wannan halin ba har na zo wuri ya k'uremin ta yadda idan na tara yara rabuwar zata min wahala idan bai sauya ba. Dum! Na ji zuciyata ta buga. Karfa naje na samu wani ciki a daren yau, na furta a zuciyata. Anya ba zan koma ba kuwa? Na tambayi kaina, ya zakiyi da tarin yawan damuwar da take zuciyar ki? Ai ko ba komai wata k'ila ki samu nutsuwa idan Allah ya sa yayi abin kirki.

Da wanann shawarar ta karshe nayi na'am da zuciyata da kuma tuna yadda idan na koma ba lalle na yu baccin kirki ba yadda nake jin marata kamar zata b'alle, sai kawai na hau gadon na gyara kwanciyata na nima na juya masa baya tunda na saba. Da zan kalli bayan sa tabbas ba zai juya ba har sai na yi bacci. Amma idan na juya baya to shi sannan zai samu damar juyowa gareni.

Cikin wasu mintina da ba su wuce uku ba wanda nake k'ok'arin na gyara kwanciya domin samun farin ciki, kawai na ji Awwal ya saki jiki yana wani irin mun shari kamar na bacci.

"Bantan uba! " Na furta cikin wata irin matsanan-ciyar damuwa. Anya Awwal yana da hankali kuwa? Wallahi ba zan yadda da wannan zaluncin ba, duk da ba yau haka ta saba faruwa ba yau kam ko ni ko shi a cikin gidannan.

"Awwal! Awwal!" Na shiga kwara masa k'ira saboda idanuna duk sun rufe yau kunyar ma babu sauranta a cikin idanuna ko ta doke yau sai ya sama min farin ciki kamar yadda ya samawa kansa. Tunda auren daman b'angare biyu ne ba shi daya ba.

Zabura yayi ya kalle ni yaha fad'in "Haba Samha, a cikin daren nan ai mak'ota ma za su ji ki wallahi. Wai tukunna ma mene ne na wannan k'iran ne hakan?"

Raina ne ya kuma b'aci da jin tambayar da ya min kamar bai san laifin sa ba. "Dole ka tambayeni tunda ka samu nutsuwa, wallahi na yi dana sanin auren ka Awwal. Kullum burinka ka soya min zuciya da mugunta?  To wallahi yau.........."

Bai bari na gama maganar ba kawai na ga ya d'auki filo ya yi falonsa. "Baka isa ba!" Na furta ina bin bayan sa.

Sai dai kafin naje tuni ya zaburo da masifa yana fad'in "Wallahi kar ki biyoni, ni matsalata da ke kenan! Sai kije kiyi wasu shaye-shayen ki kuma idan dare ya yi ki damu jama'a! To ki koma kawai bana son damuwa abin da kike so ne an yi maki to kuma sai mene ne?"

Idanu na zaro kamar yana kallona duk da cewa ya juya baya ne na ce, "Ai ba ni ce na kawo kaina ba, amma ka sani akwai gaba wallahi.

Ina gama fad'ar haka na fice a d'akinsa na koma na wa. Da kuka da addu'a da komai daren ranar na samu nacci.

Sassafe na shiga kitchen na shirya abin karyawa yana zaune a dining na same shi yana wani sussunkuyar da kai.

Solob'iyo kawai! Kamar wani wanda yayi abin arziki har yake jin kunyar ganina. Na fad'a cikin zuciyata.

Ban ko zuba masa ba na zuba nawa na fara cin ka ya na, idanu ya lumshe ya jigingina da kujerar sannan yace " Ki zubamin abinci na ci gajiya ke damuna ina son na je na kwanta."

"Dole ai ka kwana kana zikiri ai dole kaji bacci." Na ba shi amsa ina tura masa abincin da na zuba masa gaban sa. Murmushi ya yi sannan ya bude idanun sa a kan abincin ya fara ci.
Ina gamawa na shirya na fita ban ce masa komai ba na tafiyata makarantar islamiyya.

Ina chan muna karatu ya k'irani yake sanar min idan na ta shi naje gidan hajiya an yi bak'o sai ku dawo da yaran.
Bayan mun ta shi sai na koma gida tunda ya ce bak'o ai ba zanje gidan hakan ba.  Abinci na yi sannan na shirya cikin wani les na alfarma, jilbab na saka me girma na saka gilashi a idanuna na fita zuwa gidan hajiya da ke anguwar samunaka.

Da sallama na shiga gidan karon farko da wani mutum na yi idanu hud'u wanda sai da zuciyata ta tsinke da kallon da ya min. Kad'an ya hana na saki fulas d'in kayan su sube sai na ji Amira tana fad'in oyoyo Mommy......

3

Cikin sanyin jiki kamar zan fad'i kasancewar rungumar da Amira ta yi min ba ta wasa bace, sai

na dai-dai ta tsayuwar na na ce mata, "Amira sannu muje ciki ko.
Tsabar na duburburce da kallon da yake min har na mance da wani batu wai shi gaisuwa. Don haka na kama hannun Amira muka shiga ciki muka samu su hajiya a tsakar gida suna zaune ita da Shaheed da Ahamd k'annen Amira, sai kuma k'anwar Awwal mai suna Salma ita ma tana zaune.
Tana ganina ta fara murmushi ta mik'e ta karbi kayan hannun nawa ta ajjiye, zama na yi gefen hajiya ina gaida ta ta amsa min cikin farin ciki.
Salma ma ta gaida ni na amsa ina tambayar da ya bata je school ba, saboda islmiyyar mu guda da ita sai dai tana ajin farko ne.
Hira muke da sirikata gwanin ban sha'awa saboda mace ce mai kirki ba ruwanta da wani batun surukuntaka jina take kamar Salma.
"Ashe bak'o aka yi hajiya?"
Na furta cikin sanyin murya.
"Efa wallahi yaron k'anin babansu Awwal ne ya zo wanda suke abokaine daman."
Ta ba ni amsa.
"Ma sha Allah gaskiya ya yi zumunci sosai wallahi."
"Sosai kuwa aunty tun da ga abuja fa ya zo."
Salma ta ba ni amsa.
"Kai! Abuja? Gaskiya ya sha tafiya. "
"Ba kad'an ba kuwa wallahi.
Hira muke yi nida Hajiya da Salma har muka ji sallamar Awwal ya shigo.
Ban juya ba saboda ko ganin sa bana so a yanzu.
Har suka iso inda muke hajiya ta yi musu sannu da zuwa suka zauna kan ta kafet d'in.
" Samha ga nan bak'on na mu fa Mu'azzam."
Na ji Awwal ya furta.
D'ago da kaina na yi da niyyar na gaida shi kawai sai na ga wanda na gani mai shegen kallon nan ne a lokacin da na shigo .
Kuma har yanzun ma ya kureni da manyan idanun sa, gaida shi na yi ya amsa yana washe min baki.
Awwal ya ce, "Mu'azzam ka gane ta kuwa?"
"Gaskiya ban gane ta ba wallahi kasan na jima ban zo ba, Amma ko ita ce matar ta ka?"
"Au ashe ma ka gane ta ita ce aikuwa."
"Kai ma sha Allah cewa zakayi matarmu ce ai."
Harara Awwal ya watsa masa ya ce, "Da kai muka biya sadaki ne?"
"Kai Awwal  ai tunda ka biya kayi mai wuyar."

Dariya dukan su su hajiya sukayi Salma ta ce, "D'an uwa bar shi duk kishine yake damun yaya fa."
Harara Awwal ya aikamata ita ma har da jifanta da charbin hajiya ta mik'e da gudu ta shige falom hajiya .
Ganin haka ya sa na mik'e tsam na bi bayanta saboda daman na gaji da zaman.
A can falon Hajiya muka yada zango muna ta hira nida Salma har la'asar ta yi mukayi sallah muka shiga kitchen muka d'aura abincin dare.

Da misalin shida na yamma muka kammala girkin tuken shinkafa miyar yakuwa da kunun gyada na Hajiya, saboda hajiya kullum dare sai ta sha kunun gyada take bacci.

Wanke komai mukayi da muka b'ata muka gyara kitchen d'in duka sannan muka sake gyara falon muka saka turaren wuta mai d'adi sosai.

D'akin Salma muka wuce chan muka samu yaran duka sun had'e wayoyinmu suna aikin game, wanka na yi saboda matukar nayi aikin girki bana jin dad'in jikina matukar banyi wanka ba, ina fitowa Salma ta dube ni tace, "Aunty Samha kwad'uwa."

"To fa! Saboda kinganni ina lunk'aya a kogi?"
Na bata amsa ina dariya.
"Aa, kawai yawan wankanki ne yake ba ni mamaki. Ke fa kullum kika zo mukayi girki da ke sai kinyi wanka a gidan nan."

"Ai Salma wanka duniya ne wallahi, kuma matukar kika yi aikin girki to kawai kiyi wanka kar ki ce wai ai mukubur ne ko gas, a'a shi kansa wannan hayakin dake fita a cikin abincin ai duka kamshin sa jikin ki zai turara, to kinga bai kyautu ace ke da abincin kuna kamshi guda ba. Amma idan ki kayi wanka kika sha k'amshi to abinci daban ke ma daban."

Baki Salma ta sake ta na kallona tace, "Ai kuwa dai gaskiya ne, sai dai ba kowacce mace ce zata iya hakan ba sai Irin ku gaskiya, ina yiwa ya ya murna ya samu mace ta gari kuma mai addini."

Murmushi na yi da yabon da ta yi min na ce, "Kai Salma wallahi baki da dama."

"Kai aunty ina da mana tunda ga shi har abinci nake ci da ita."

Da hararar wasa na bita na saka kaya muka fita falo domin yin sallar magrib, muna zuwa muka ga Hajiya tana kan sallaya tana lazimi ita da Amira.

Su Shaheed kuwa na san sun tafi masallaci.

Kowa sallah ya fara yi jin an gama k'iran sallar magrib d'in.

Sai bayan isha tukanna su Awwal da Mu'azzam suka shigo suka zauna da nufin cin abinci.

Nan falo muka shirya komai ni da Salma muka zubawa kowa ya fara ci.
Can sai Mu'azzam ya yi gyaran murya tare da fad'in, "Um na ce ba."
"Muna jinka." Salma ta ba shi amsa.
"Yawwa Salma wai wace ce ta yi wannan abinci mai shegen dad'i?"
Dariya Hajiya ta yi ta ce, "Allah ya sa dai Mu'azzam kana kusa da kujera."
"Gaskiya kam."
Awwal ya furta.
"Ya Mu'azzam ai matartaku ce ta girka."
Salma ta fad'a.
"Kai! Yanzu Awwal saboda rashin mutumci matar ta iya wannan girkin shine ba ka gayyace ni da sallah ba?"
"To yanzu da gulmarka ta motsa ba gashi ka zo ba kuma ka ci."
Awwal ya ba shi amsa.
Hajiya kuwa cewa tayi ita yaronta ba gulma yazo ba zumunci ya zo. Haka dai sukayi ta raha har muka gama.

Sai wajen tara tukunna muka fara haramar tafiya gida, Mu'azzam ya dubi ne ya ce, "Matar gaskiya ranar da zanzo atabbatar an yi mana girki wanda ya fi wannan ma dad'i."

Kallo na kai ga Awwal na ga yadda ya had'e fuska da alamu baya son ya k'irani da wannan sunan.
Ganin hakan da nayi ni kuwa tuni na sake fuska tare da fad'in, "Karka damu, in sha Allah duk yadda ka ce hakan za'ayi."
Washe baki Mu'azzam ya yi ya na fad'in, "Godiya nake ginbiyarmu."
Daga haka Awwal ya sa ke b'ata fuska ya fice a gidan.
Bayan sa muka bi dukan mu har Hajiya har sai da muka shiga ya tayar da motar sannan suka juya cikin gida.

Sassafe da gari ya waye na shirya yara da yakr monday ce suka ta fi School. Ina kwance a falo ina hutawa sai ga shi ya shigo gidan fuska duk a chakud'e ya dube ni ya ce.........

4

"Wai ke da ga kinga maza sai kiyi ta washe baki saboda rashin hankali, har ya na ce miki matar kina wani washe baki ko? To wallahi karki ga d'an uwa na ne duk wanda zai shiga gona ta zan ragaraga da ke da shi d'in."
Ni maganar ta sa ma dariya ta ba ni, don haka na tik'i dariya sosai iya san raina har da tuntsurawa sannna na dube shi ya cika ya kai iya wuya, na ce, "Ragaraga ko? Su Awwal manyan mazaje."
Ina fad'ar haka na mik'e na yi hanyar d'akina.
Da sauri har da sassarfa yake biyoni, ni kuwa ganin haka sai na arce da gudu na shiga na saka sakata.
"Ki bud'e mana! Ai da na koya miki hankali, ina magana kina dariya kamar kin samu sa'anki?"
Ina daga ciki na ce, "Haba mazaje kamar ka ai ba duka aka sanku da shi sai dai gwaninta da nuna isa a inda ya da ce."
"Mazaje!!" Na furta da k'arfi tare da sake kwashewa da dariya ba wai don ina jinta ba.
Kwafa ya yi ya bar wurin ina jinsa.
Bakin gadona na koma na yi jigum ina tuna yadda Awwal ya nuna min zallar k'auna a lokacin da yake sona, wanda hakan ne har ya sa na bijirewa zabin da na yi a farko wanda har na nuna shi a gida.
Ba zan mance lokacin da muke 'yan mata ba, watarana mun ta shi a makaranta ni da k'awata kulsum muna sanye cikin uniform na kayan gammande kuma a lokacin muna aji uku wato matakin k'arshe na gamawa. Kasan cewar ana zafin rana ga shi yau mun sha duka a wurin wani malamin mu dalilin rashin yin aikin gida da yabu, shine ya sa na ce da kulsum yau sai dai mu ne mi mashin ya kaimu gida don ba zan iya tafiya ba, har wani jiri nake ji idan na mik'e .
Tsaye mukayi bakin hanya muna duba na mashin wanda zamu hau amma wayam ba kowa .
Kusan minti goma muna tsaye har na fara jin juya ta na d'ibata, don haka sai na jingina a jikin wata bishiya.
Mashin muka hango yana zuwa inda muke, don haka sai muka shiga tsaida shi. Sai da ya zo daf damu sai muka ga ashe Isa saurayina ne. Wata kunya ce ta lullub'eni ganin irin murmushin

da yake sakar min tare da kashe min ido d'aya.
"Samhata yau kuma me ya faru kuke tsaye haka anan?"
Jin na yi shuru ne ya sa Kulsum ta ce, " Isa wallahi masiyiyarka ce ta tsaida mu wai ba zata iya tafiya ba sai a mashin."
"Fad'uwa Ta zo daidai da zama. Kinga yanzu sai ta hau na kaita na dawo kema na d'auke ki."
Isa ya furta yana me kallona.
"Cab! "Shine abin da na furta tare da fara jan k'afata domin ko giyar wake na sha ba zan tab'a hawa bayansa ya goyani ya kaini gida ba.
Ganin haka tuni kulsum ta ce, " Ai daman na san za'ayi haka, ba za ta hau ba fa."
"Wai kina nufin Samhata ba zaki hau ba?"
Ni dai ban kula shi ba na mak'e kafad'a na yi gaba.
Lallashin duniya Isa ya yi amma sam na k'i hawa. Don haka dole ya hak'ira ya tafi ya barmu. Daga haka ba mu kuma jiran abun hawa ba muka kama hanya har gida.
La'asar sakaliya ina yiwa mama gyaran kayan miya za ta d'aura miya sai ga yaro ya yi sallama wai ana k'irana a waje.
Ko da jin haka tuni na san cewa Isa ne. Wani farin ciki ya mamaye min zuciya saboda ina matuk'ar kaunar Isa a zuciyata sosai, amma duk da haka ba zan iya fita ba sai mama ta bayar da izini Saboda ina jin kunya.
Kusan minti biyar mama ta ce, "Samha ba jiran ki ake yi ba ne?"
Ban ce komai ba na ta shi simi simi na yi falonmu na kuma gyara fuskata da hota da kwalli. Turaren mama na fesa mai kamshi na zura hijabina na fita domin na same shi. A zauren gidanmu na same shi tsaye har ya gaji da tsayuwa ya tsugunna. Da sallama na shigo a bakina ya dube ni yayi mirmushi ya ce, "Wa'alaikissalam ya ke ma'abociyar k'amshi da shanya mutane."
Murmushi na yi na sa ci kallonsa na ce, "A'a fa dai, ba shanya ba ce."
"To mene ne?"
"Ina yini, kawai mu gaisa kafin."
"Wato kina nufin a bar zancen ko?"

"Kamar haka dai."
Na ba shi amsa
"Wai Samha sai yaushe zaki daina jin kunyata ne?"
Isa ya tambaye ni. "To ai dole na ji kunyar ka." Na furta cikin shagwaba tare da turo baki gaba.
"Me sa to ?"
"Saboda kai d'in kai ne mijina, nan gaba."
"To yanzu idan munyi auren ma kunyata zaki na ji?"
"Uh uh ni dai a bar maganar kawai."
"Samha sarkin kunya, Allah dai ya sa ba zaki juya min baya ba har gaban abada, saboda wallahi samha ina matuk'ar k'aunarki a zuciyata, Samha k'aunarki fa ta kai girma da ko cikin dare na kan iya farkawa na saka hoton ki gaba ina kalla ina hawaye ba don komi ba sai dan tsabar yadda zuciyata da numfashina suke fusgowa ta dalilinki. Samha ina k'aunarki k'aunar da bazan iya yiwa wata mace a duniya ba.
Idan na rasa ki wallahi na san zayyi wuya na rayu, ke ko da na rayu ma ba lalle na yi amfani

ba. Saboda ko da yaushe lumfashima da soyayyar ki yake fita. Don Allah Samha ki kasance tare da ni har karshen rayuwata."

Ya k'arashe maganar cikin wata irin murya wacce ban san shi da ita ba, daga inda na ke kuwa ina iya ganin yadda lumfashinsa yake harbawa sosai da sosai.

Ni kuwa hawaye tuni ya wanke mun fuska da jin kalmansa, dukkan lokacin da za'a furta mini kalmomi irin haka to suna ratsa min zuciyata na ji kamar a wata duniya nake.

Ka sa cewa da shi uffan na yi kawai sai zauna daram .

Shi ma zaman ya yi ya kuma cewa, "Samha ki ce wani abu mana."

Gyara zama na yi sosai na ce, "Yaya, wallahi baki ya yi k'an wajen furta kalar kaunar da nake maka sai dai na ce komai wuya muna tare in sha Allah.

Da haka mukayi ta hira jar kusan magrib sannan ya tafi na koma gida. D'aki kai tsaye na wuce na kwanta kan gadon mama, haka kurum kalaman sa suke dawomin a zuciya ina hawayen da na gaza na farin ciki ne ko akasin sa? Wasa gaske soyayay ta yi nisa tskaanina da Isa kwatsam wata rana muna zaune inda muka saba zance sai ga yaya Harun ya dawo daga tafiya, duban mu ya yi bayyi magana ba ya wuce. Sai dai irin kallon da yake min shi ne ya sanya na ji duk hankalina bai kwanta ba. Ganin na shiga damuwa sai Isa ya sallame ni na koma gida.

Bayan sallar isha mama tace min baban mu yana k'irana.

Zuciyata sai da ta harba da jin k'iran duk sa cewa ban san akan mene ne kiran ba. Baban mu mutum ne me sauk'in kai wani lokaci kuma me fad'ane. Ya kasan ce laccara ne mai koyar da ilimin lissafi, mahaifiyarmu ita k'ad'ai ya aura, ita kuma mu biyar ta haifa. Yaya Yusuf shine babba, sai Yaya Sadik ya ke binsa, sai kuma Aunty hannatu Sai Aunty Dija, Sai ni autar su.

Kuma dukan su sun kusa kammala karatun su kuma kowacce acikin su an saka mata ranar aure wacce rana guda ce za'ayi bikin.

Yaya Yusuf kuwa bayyi aure ba bare Kuma Yaya Sadik.

"Samha!"

K'iran da mama ta yi min ne ya sa na mike da sauri na saka hijabina domin na amsa k'iran da baba ya min.

Ko da na shiga falon sa duka yayyuna suna zaune a gaban babanmu. Wani irin fad'uwar gaba ce ta riskeni da na ga irin Kallon da Yaya Yusf yake min.....

5

Wuri na samu na zauna daga gefe guda na fara gaidasu d'aya bayan d'aya. Abbanmu ya dube ni ya ce, "Mamata, kinga yaron nan da yake zuwa wajenki, idan har da gaske kina son shi yana sonki to maza ki ce ya turo da iyayen sa, saboda idan har da gaske yake zan had'a aurenki da sauran 'yan uwanki ne tunda saura k'iris ya rage ki gama kya cigaba da karatun na ki a gidan sa."

"Ajjiyar zuciya na sauke ina jin wata kunya tana lullub'eni. Yanzu kuma taya za'ayi min aure ban yi jami'a ba? Kuma shi kansa Isa ba ni da tabbacin zayyi auren yanz.....tswar da Yaya Yusuf ya daka min ce ta sa na firgita na d'ago da idanuna na du be shi.

" Ba magana aka miki ba ne ki ka yi shuru! Ko akwai abokin wasan ki anan?"

"A'a Ya ya, in sha Allah zan sanar masa da zarar ya dawo."

"Yawwa Mamana hakan ya kamata ayi, ta shi kije abin ki."
Abbanmu ya furta.
Mik'ewa na yi har ina sassarfa na bar wurin na koma d'akin mama.
Ban san me suka tattauna ba ni dai naga su Aunty sun dawo sai murna suke suna tsalle.
Kwana uku rabona da Isa kamar ya ji labarin abin da ya faru ko kuma nake son sanar masa, kuma ba ni da waya bare na k'ira shi.
Haka na HaKura
Ranar monday muna tafiya makaranta ni da k'awata muka ga ganshi ya wuce a mashin bai ganmu ba, sai sannan na samu nutsuwa da na tabbatar da lafiyarsa kalau. Haka mukayi karatun amma duk hankalina yana kansa, har na fara jin damuwa ta mamaye min zuciyata. Domin bai saba kwana biyu bai ziyarce ni ba, ko kuma ya aikomin da sak'on wasik'a. Amma shuru sam ba kansa kuma lafiyar sa kalau.

Ko da muka dawo gida yamma ta na yi muka tafi islamiyya ni da yayyuna,
Sai wajen shida aka ta she mu, Aunty Dija ta dubeni ta cd, "Ke wai me ya same ki ne tun da rana na ganki wata k'ala?"
"Babu komai kawai kaina ne yake ciwo."
Na ba ta amsa. Sai ta ce da ni ya kamata daga mun koma gida na sha magani kar abin ya yi nisa.
Da to na amsa mata muka ta fi gida. Muna zuwa na tarar da takardar da nake saka ran zuwanta ta wasik'a yaro ya kawo bana nan.
Har ina washe baki na mance a gaban su Mama na ke. Su kuwa su aunty Dija kallo suka bi ni da shi. Ta kardar ta amsa na wuce d'akin mama na fad'a kan gado wani shauk'i yana d'ibana tun ban bude ba.
"Abar k'aunata abar sona, sanyin idaniyata annurrin zuciyata, macen da babu kamarta binni da k'auye. Hak'ika zuciyata ta azabtu da rashin ganinki, hancina ya yi kewar k'amshinki. Idanuna sun yi kewar ganinki. My Samha, bakina ba zai iya sanar miki da tarin k'aunar da nake miki ba. Na san kinyi mamaki da jina shuru ban zo ba, ina mai baki hakuri da hakan, hakan ya faru ne sakamakon rashin lafiyar da nake fama da shi. Yanzu haka ina asibiti a kwance. Tun ranar da na ganki ban tsaya ba saboda baba yana jirana a ranar. Daga masoyinki Isa."
Ina kammala karantawa na rugume takardar a k'irjina na fashe da kuka ina fad'in, "Daman na san zayyi wuya ace kana lafiya baka zo ba."
Allah Allah nake gobe ta yi na fita makaranta daga an tashi goma na je na duba shi tunda ba nisa da makarantar.
Bayan munyi sallar magarib duka muka hallara karatu a falon baba, anan ma sai da aka ritsani da tambaya amma ban ce komai ba. Saboda da zarar an fara min tambaya daga bakin mutanen da ya wuce biyu sai naji kuka yana zuwamin ni haka nake daman.
Da sassafe na shirya na fita makaranta, tun kafin mu shiga aji na sanar da Kulsum zata min rakiya asibiti dubiya.
Ta amsa min da to ba damuwa. Muna karatu ina duba agogon Ta kusa dani da yakr ita ce mai buga k'ararrawa. Wata irin mummunar fad'uwar gaba ce ta riskeni na fara ambaton sunan Allah.
Ana fita kuwa ban bari mun ci komai ba na d'auki kaltum muka fita, muna shiga ba mu sha

wahala ba da yake d'akin maza ba shi da nisa sosai. Sai dai abin da idanuna suka ganemin ne ya sani tsyawa cak!
Wasu maza ma gani suna rike da hannun isa ba ya iya ko lafiya an d'aura shi a kan kujerar da ake tura marasa lafiya za'a kaishi wani waje. Wasu hawaye na ji masu zafi suna zirtatowa daga cikin idanuna. Yana d'ago da kansa muka had'a idanu. "Samha."
Ya furta cikin sark'ewar murya. Ban iya amsawa ba saboda idan na ce zanyi magana kuka zanyi. Da yake maganar a hankali ya yi nima dan ina ganin bakinsa ne na san me ya fad'a ba wanda yaji, sai kawai suka tura shi suka tafi da shi. D'akin tiyata na ga sun nufa ni dai ban san me za'ayi masa ba.
Kaltum ta yi yin duniya mu tafi na ce sam! Ina nan ta koma kawai ni sai na ga fitowar su. Da k'yar ta lallab'ani muka fara tafiya, bamuyi nisa ba na ji an k'ira sunana daga bayan mu, cikin san in san me k'iran ya sa ni na yi saurin juyawa.......

6

Ina juyawa sai na ga abokin Yaya Yusuf ne, gaida shi na yi ya amsa ya na tambayata wa ye ba lafiya. Duburburcewa na yi, sai Kaltum ta yi wuf ta ce, " Rakoni ta yi dubiya." Wani sanyi na ji da jin batunta ina me farin cikin kub'utar dani da ta yi, domin kuwa mutum ne me bin kwakwaf, kuma na san zayyi wuya bai sanar da Yaya Yusuf had'uwar mu ba.
Shi yasa gaba d'aya na gaza nutsuwa. Da haka dai muka wuce shi a wurin, ko da muka koma school d'in ban fahimci komai ba har aka ta shi. Ina zuwa gida kuwa na yi sauri na yiwa mama bayanin cewa na raka Kaltum dubiya Asibiti gudun kar Yaya Yusuf ya tuhume ni. Kamar kuwa na san haka za ta faru, bayan magrib yana shigowa gida tambayar da ya fara min kenan. Amsar da na bashi tilas ta sa ya hak'ura.
Bayan mun kammala karatun dare sai na koma d'akinmu domin na lallab'i zuciyata da damuwa da take damunta. Yayuna suka sani gaba da tambaya dole na sanar musu gaskiya tunda ba ni da wanda suka fi su a yanzu. Aunty Dija ta rik'e hab'a tare da fad'in, "Ohh Allah, yanzu Samha har kinyi girman da za kiyiwa soyayya kuka?"
Ban iya bata amsa ba kawai na ci gaba da kukana.
Haka na kwana cikin damuwa ina jin yadda zuciyata take bugawa da sauri da sauri. Da wuri na shirya muka tafi School domin yau so nake kafin a shiga aji ma na duba shi. Muna shiga cikin asibitin sai muka ci karo da wasu daga cikin danginsa suna zubar hawaye, cike da damuwa na tare wata daga cikin su ina tambayar ta ko lafiya, tare da ce mata ina Isa ya ke ya kuma jikinsa.
Amma shuru ba amsa. Ganin na kid'ime sosai shi ne ya sa wata daga cikinsu ta ce min, " Yarinya kiyi hak'uri yanzunnan Isa Allah yayi masa rasuwa, kuma har ya kusa rasuwa yana fad'in sunan wata Samha, wannan shine abin da ya damemu. Muna son mu san ko wacece ko tana binsa bashi ne yake so ya ce."
Tun da ta fara maganar na ji wani irin abu ya sauk'a a jikina me kama da tafashashshen ruwan zafi ya gigita dukkan nutsuwa ta. Wata furgitacciyar kuwwa na saki na zube sumammiya.
Ban san me ya faru ba
Sai da na bud'e idanuna na ganni a kwance a gadon Asibiti, gefena Kaltum ce da wani wanda ban san shi ba.

Ganin na farka ya sa Kaltum cewa, "Alhmdulillah! Samha don Allah bud'e idanunki sosai, ba gaskiya bane abin da ta fad'a."
Girgiza kai nayi wasu hawaye suna kawo ziyara kan fuskata masu zafin gaske, tare da wani mummunan ciwon kai da yake ratsa dukkan jikina.
"Kaltum." Na k'ira sunanta cikin raunatacciyar murya.
Amsawa ta yi tare da matsowa kusa dani sosai. "Ai ba yadda za'ayi bai rasu ba su ce ya rasu. Tabbas Isa ya rasu ya barni da tarin k'aunar da nake masa, ya bar zuciyata da muradin son ganinsa, ya barta da batutuwa da nake son na furta masa. Ina jin ceqa tabbas ba zan yi nisan kwana ba zan mutu."
"Haba ke kuwa, me zai sa ki ce haka? Idan Allah ya karb'i wani bawa ba yana nufin wani bawa ba zai rayuba sai da wannan d'in."
Na ji sauk'ar maganganunsa a cikin kunne na.
Ban ba shi amsa ba saboda ganin ya min kwarjini, sai Kaltum ce ta ce da shi, "Haka ne."
Sannan ta dube ni ta ce, "Samha wannan mutumin shi ne ya taimake ni da motarsa a lokacin da kika fad'i har zuwa bakin titin da d'akin nan yake. Kuma shine ya tsaya a kan mu ganin ba kowa kusa damu har aka baki kulawa ta musamman."
Kai na jinjina sannan ta dube shi na ce masa, "Mun gode sosai."
"Babu komai." Ita ce amsar da ya ba ni.
Har wajen azahar ina kwance a gadon asibiti na ce wa Kaltum lalle lalle ya ka mata mubar asibitinnan tun kafin asirina ya tonu, domin ta san halin 'yan gidanmu indai mutum ya aikata wani abu a b'oye to ya shiga uku. Bare kuma ni da na zo duba saurayi duk da cewa ya bar duniya ban sani ba ko alhinin hakan zai sa a rageni da fad'an idan anji.
Da to ta amsamin ta dubi wannan bawan Allah da ta ce ya taimakemu tace masa zamu tafi gida gaskiya saboda akwai matsala.
Ina ji ya tambayi Kaltum mene ne matsalar ta sanar masa komai ba ta b'oye mishi ba. Jinjina kai ya yi ya fita can sai suka shugo shi da wani likita ya du ba ni ya kuma tabbatar masa da zamu iya tafiya, amma da sharad'in na kula da shan magani. Da to ya amsa masa Na ta shi zaune Kaltum ta taimakamin muka fita. Bayan mu ya bi yace da Kaltum idan ba damuwa zai kaimu gida saboda yanayin jikina ba kwari, kuma ko mashin muka hau ba zamu samu nutsuwa ba. Ba ta yi masa musu ba kasancewar ta san ban cika son hawa mashin ba in ba dole ba. Ban yi musu ba ni ma saboda na san ba zai cutar damu ba in sha Allah, tunda har ya taimake mu.
Don haka muka shiga motarsa ya d'akko mu har wajen layinmu na ce ya tsaya anan mu sauk'a.
Bai musa ba ya tsaya tare da min fatan samun lafiya.
Fita muka yi nida Kaltum muka do shi gida, sai dai ina d'ago da kaina na yi idanu hud'u da Babanmu da Yaya Yusuf suna zaune k'ofar gida suna kallonmu ni da Kaltum. Wata irin fargaba ce ta riski zuciyata wacce sai da ta yi sanadiyyar zubar wasu hawaye daga idanuna tare da fad'in "Na shi ga uku na kaltum.
Dubana ta yi tace karna damu ta san abin da za ta ce kawai na yi maza na goge hawayena.
Gogewa mukayi muka k'arasa inda su Babanmu suke fuskokin su duka cike da alamar tambaya.
Firgigit na dawo daga duniyar tunanin da na tafi jin ana ta bugamin k'ofar dakina. Muryar Ameera da na ji shine ya tabbatar min da sub dawo a makaranta ko abinci ban samu na yi

musu ba. Da sauri na bud'e k'ofar na yi musu sannu da dawowa na ce su je suyi sallah ina zuwa zanje kitchen, sauri sauri na shiga na d'aura mana jalof d'in taliya domin zan fi saurin gamawa. Ina tsaka da girkin sai na ji kamar motsin mutum a bayana. Sauri na yi na juya domin ganin waye ne. Awwal ne tsaye ya ware min hannaye da nufin na zo ya rungume ni. Mamaki fal ya mamaye min zuciya, "Wai anya Awwal ne kuwa? Ko dai mafarki nake yi ne?" Na tambayi kaina. Cikin tsoro nake kusantowa gareshi tare da k'okarin murmusawa saboda zuciyata idan ta samu abin da take muradi, mancewa take da dukkan kuskuren da Awwal ya turnuk'amin.

Sai dai ina zuwa daf da shi zan fad'a jikin sa ya ja gefe na gwaru da bangon wurin, take bakina ya fashe a wurin. Shi kuwa juyawa ya yi bai ce komai ba ya fice. Mamaki da Al'ajabi sune suka saka ni na gaza cewa komai. A halin yanzu a furgice na ke da wurin ma sosai. Da kyar na iya kammala komai na fita a kitchen d'in, sai dai ina zuwa falo na ci k'aro da shi zaune yana min murmushi. Wata kyakkawar ajiyar zuciya na sauke wacce ta yi sanadin da Awwal ya kalle ni ya kuma mun murmushi. Sakin abincin na yi na wuce d'aki da mugun gudu na rufe ina salati domin tabbas na san na yi gamu.

A falo kuwa Awwal ne zaune yayi dariya son ransa tare da fad'in Samha zan koya miki hankali.............

7

Wani irin tsoro sosai ya riski zuciyata, damuwa da tunanina Allah ya sa ba gamo na yi ba. Ina jin yadda su Ameera suke bugun k'ofar suna cewa na bud'e Abban su ya dawo abincin bai zube ba. Fad'in ya dawo shine ya kuma rikita ni. Ke nan da gaske dai gamon na yi ba Awwal bane. Cike da damuwa na yunk'ura na bu de k'ofar na fita zuwa falo ina rak'ub'ewa kamar wata munafuka. Kallon sa na yi ya had'e rai gyam yana hakimce a kujera amma ba wacce na barshi ba. "Tabbas wannan shi ne Awwal mijina." Na furta a cikin zuciyata. Domin Wancen Awwal d'in ma'abocin murmushi ne, na wa kuwa ga kalar sa nan. "Wai tsayuwar me kike ne ba zaki zuba mana abinci ba!" Ya fad'a cikin tsawar da ta yi sanadin zaburata izuwa dining. Abin ka da mai zaman jiran kiris.

"Tofa! Yau kuma wani sabon salo kika zo da shi gidan." Awwal ya fad'a.

Ban kula shi ba har na je na gama zuba komai na zauna ina ganin yadda suke cin abinci cikin kwanciyar hankali amma ni kuwa sam bani da ma kwanciyar hankali bare na yi tunanin wata aba wai ita yunwa. Ganin ba na cin abinci ne ya sa Ameera ta fara cewa, "Mama, ki ci abinci mana ya yi dad'i fa." Kallon ta kawai na yi na gyada kai na kalli inda Awwal yake zaune yana cin abinci bai ko kalle mu ba. Ina ganin ya mik'e ya yi hanyar d'akin sa na bi shi. Domin ji nake matukar ya ta fi to aljanin sa zai fito. Ganin ina bin sa ne ya sa ya juyo tare da fad'in , "Malama lafiya kike bi na?"

Turus! Na ja na tsaya na rasa abin fad'a. Ina ganin ya ci gaba da tafiya na kuma binsa har muka shiga d'akin sa. Zama ya yi a bakin gadonsa don haka na yi saurin zama gefen sa tare da rungume shi k'am k'am na ce, "Bombino, don girman Allah kai ni gidan hajiya, wallahi ba zan iya zama a gidannan ba. Ko kuma ka kaini gidanmu amma wallahi zai illata ni."

Chakume fuska ya yi ya fara ki ci niyar raba ni da jikin sa ya ce, "Samha mene ne haka wai? Ki bar jikina fa ban son rashin hankali, wa ye zai illata ki a cikin gidan bayan mu kad'ai muke a

cikin gidan?" "A aljanin ka wallahi! Aljanin ka ne zai ka she ni ."  Na ba shi amsa tare da rushewa da kuka. Madubi na kalla sai kuwa na ga Awwal a ciki yana murmushi. Sam na mance cewa ni da shi duka muna agaban madubi ne . Wata uwar k'ara na sa ka tare da zubewa a jikin sa sumamma. Wuraren la'asar sakaliya na farka na ganni kan gadona ni guda ina kwance zabura na yi na yo falo na tarar ba kowa domin na san yaran duka suna islamiyya. Da sauri-sauri na rufe gidan na shiga gidan mama Aisha mak'ociyata na kai mata ziyarar dole. Hira muke amma sam hankali na baya kan zancen, har ta fuskanci ina cikin matsala. Ko da ta tambaye ni me yake faruwa da ni na ce mata ba komai. Ana shirin k'iran sallah na fito na zo zan bud'e gida sai ga Awwal ya dawo da yara. Don haka tare muka shiga da su, sai sannan na ce da Ameera ta rakani kitchen na daura abinci. Shi dai kawai kallona yake yi.

Haka muka d'auki tsawon mako biyi kullum cikin fargaba nake rayuwa a cikin gidan duk da cewa ban kuma gamo da aljaninn Awwal ba.  Ko makaranta ba na iya zuwa har su adama suka min waya na sanar musu zan fito satin gaba.

Satin gaba da ya gabata na samu zuwa makaranta amma sam ba na cikin nutsuwata, saboda ban gama sakin jiki da gidan ba, kuma ga shi ina cike da matsananciyar sha'awar da ta ke son ta fi k'arfin tunani da hankali na. Ina mamakin kaina idan aka cire kwanakin da na yi jinyar jinnunna kullum sai na ta shi cikin dare na sanarwa Allah a mai dani kalar Awwal ko kuma shi a mai da shi kalata. Amma sam ban samu sauyin ko guda daga ciki ba. Sai ma yadda na fuskanta abin na wa kullum ci gaba yake yi.  Daga makaranta gidanmu na wuce ranar wurin mamata domin ko ba komai ya kamata ta san halin da nake ciki.

Ko da na sanar mata halin da nake ciki game da Aljanin Awwal. Murmushi Mama ta yi tace dani kawai na tsorata ne ba wani aljani abin da take so dani kawai na rik'e addu'a.

Haka dai muka yi ta tattaunawa tana k'ara sanar min wasu addu'o'in da ban san su ba na neman tsari da jinnu. Misalin biyar na koma gida na  saki jiki na shiga kitchen d'in da rabon da na shi ge shi ni kad'ai tun ranar da abin ya faru. Bakina cike da addu'o'i har na kammala komai na dawi falo na kunna k'iara'ar alkur'ani mai girma sautin suratun bak'ara daga bakin Aramma malam Abdurrahman Yola. Yana yi ina bi har lokacin sallah ya yi Awwak ya dawo da yara. Haushin sa ne ya kamani ta yadda yake yawo zulum-zulum cikin maza yana amsa sunan su, alhalin shi rakosu ya yi. Bayan munyi sallah sai muka ci abinci da yarana ban da shi saboda ya fita. Aikin gida na taimaka musu suka yi har aka kira sallar isha. Sallah muka yi sannan na kaisu d'akin su ka kwanta. Ita kuma Ameera a kusa d'akina nata d'akin yake.

Falo na dawo ina zaune ina kallon tashar zee aflan wani indiyan fim ake haskawa na soyayya na yi nisa sosai da shagala a cikin kallon sa yadda jarumin yake nunuwa jarumar kulawa da soyayya shine ya ba wa zuciyata damar aikewa da kwakwalwata katin gayyatar dawomin da bara bana.....

Yaya Yusuf ne ya kalli Kaltum ya tambayr ta daga ina muke kuma waye ya sauke mu. Baba kuwa bai ce komai ba ya tsaya na k'are min kallo. Duk na firgice amma kuma da jin amsar da Kaltum ta fara bawa Yaya sai na samu nutsuwa.  "Bayan mun fita munje makaranta sai na ce da Samha ta rakani na siyo biro a wani shago bakin titi, muna fita sai wannan me motar Allah ya kawo tsautsayi na buge Samha amma kuma bata ji ciwo ba sai suma da ta yi saboda firgici. Ganin haka ya sa aka shigar da ita mota nima na shiga ya kaimu asibiti aka bata kulawa. Ko da ta farfad'o  aka tabbatar ta samu nutsuwa kuma bata da wata damuwa shine aka sallame mu, sai ya kawo mu gida Samha ta ce ya sauk'e mu bata son ku ji kar hankalin ku ya ta shi."

Kaltum na kaiwa karshen zancen ya ya Yusuf ya mike a fusa ce tare da fad'in, "Kuma shi ne ya biye mata ba zai zo gida ya bayar da hakuri ba? Zaki iya gane lambar motar sa?" Ya tambayi kaltum. Wani sanyi na ji ya ratsa zuciyata yadda na ga yaya Yusuf ya yarda da maganar kaltum. "Gaskiya ba zan iya ganewa ba, saboda agigice na ke wallahi."
Kaltum ta bayar da amsa.
Ya ya Yusuf ya ce, "Baba bari na bi sawun sa ko zan tarad da shi ."
"Aa Yusuf bar shi kawai tunda dai har ya kaita asibiti an duba lafiyarta ai zance ya k'are. "
Fa sa tafiyar yayi ya juyo ya kalle ni ya ce, "Yanzu ba in da yake miki ciwo?"
Kallona na kai gare shi na ce, "Eh Yaya."
To shi ke nan ku shiga ciki kawai. Ya bamu amsa. Shiga muka yi muna Sallama ba kowa tsakar gidan don na tabbata su aunty ba sa gida mama kuwa a wannan lokacin ta na Sallah da na filfili.
Muna shiga d'akinmu na fad'a gado na fashe da kuka na ce, "Yanzu Kaltum shi ke nan na rasa Isa? Isa ya barni da duniya wayyoa zuciyata , Kaltum Isa ya mace ya barni da tarin soyayyar sa a zuciyata."
"Haba Samha ki yi shuru mana kar wani ya ji ya gane gaskiyar da muka b'oye. Ki yi hakuri yanzu ba lokacin kuka bane, lokaci ne da zakiyi masa addu'a, a yanzu Isa yana can yana amsa tambayar da mala'iku suke masa... Ko da jin haka wani sabon kuka ya zo min na danna kaina cikin fulo ina yin sa gudun kar wani yaji ya tambayi ba'asi.
Haka dai kaltum ta lallab'ani ta bar gidan. Kusan kwana biyar da faruwar hakan Babanmu ya k'irani ya kuma sanar min na sanar da me zuwa wurina fa idan ya zo. Sanar masa na yi da ya rasu ma shi baya duniyar, hankalin Babanmu kwarai sai da ya ta shi da jin mutuwar Isa. Fatan rahma ya yi masa sannna ya yi mun addu'a da fatan samun wanda ya fi shi.
Kwanaki na wucewa watanni na shud'ewa shekaru na taruwa. Kwatsam watarana aka turo yaro aka ce ana sallama da ni a k'ofar gidanmu. Koda na fita sai da zuciyata ta buga saboda ganin me k'iran........

8

Ganin sa ba k'aramin tayar min da hankali ya yi ba, domin ya dawo min da mutuwar Isa ne sabuwa dal! Cikin zuciyata. Wannan bawan Allahn nan ne da ya temake ni a lokacin mutuwar Isa. Kamar me sand'a na k'arasa wurin sa da sallamar da da kyar ake iya jiyota a gare ni.
Amsa min ya yi cikin farin ciki sannan ya gaidani tun kafin na gaida shi. Amsa masa na yi cike da jin kunyarsa, saboda ni ce ya kamata na gaida shi .
Shuru muka yi dukan mu na wani lokaci sai can kuma ya ce dani, "Tun da na ta fi na gaza samun sukuni, ina ta tunanin ko ya jikin ki. Amma sam zuciyata ta gaza samun sukuni shine na ce bari na zo na duba lafiyarki."
"Ayya, gaskiya na gode sosai da kulawarka Allah ya bar zumunci."
"Amin." Ya amsamin ya kuma tambayata Kaltum. Sai na sanar masa tana gidan su yau ba mu had'u ba. Mun dan tab'a hira kafin ya yi min ban kwana ya tafi ni ma na koma gida.
Daga haka wasa gaske k
Duk bayan wasu kwanaki sai ya zo mun gaisa har ranar na fidda kunya na tambaye shi

sunansa ya ce da ni Awwal. Abu guda da Awwal ya furta a gare ni shi ne ya yi silar watsewar tarayya ta da shi. Muna tsaye muna hira kamar kullum ni da shi ya du be ni ya ce, "Samha, yaude ya kamata na bud'e miki sirrin zuciyata ki sani tunda dai na ga kin gaza fahimta."
Ban kawo komai ba a zuciyata na ce, "Yaya Awwal ina jinka."
Murmusawa ya yi ya kalle ni ya gyara zama ya ce, "Wato Samha ranar da na fara ganin ki na tausaya miki sosai fiye da yadda zaki tsammata. Zuciyata ta yaba da ke sosai da jin cewa na samu matar aure, sai dai bayanin da k'awarki kaltum ta yi min a asibiti shi ne ya dakatar dani da abin da ya ke zuciyata. Amma zuwa yanzu ya kamata ki san cewa Wallahi ina matuk'ar kaunar ki sosai a zuciyata. "
Tun da ya fara magana nake jin sa, yana kawo k'arshen zancen na sa na ji zuciyata tana min wani irin d'aci. "Awwal ka yi hakuri zuciyata ta Isa ce shi kad'ai, yadda ya mutu ya barni ina jin cewa ba zan wani jima ba ni ma zan bi shi." Ina gama fad'ar haka na mik'e na shiga gida. Wasa gaske tsawon mako biyu dukkan sanda ya aiko yaro bana fita har mama ta fahimci da matsala ta zaunar da ni ta tambaye ni ba'asi. A maimakon na ba ta amsa kawai sai na saka mata kuka, ba ta hanani ba sai da na yi don kaina na gama sannan ta ce dani tana ji na.
Kwashe dukkan abin da ya faru na yi na sanar mata har k'aryar da muka yi ni da Kaltum ranar da Isa ya rasu. Mama ta yi min fad'a sosai kan hakan sannan ta nuna min cewa matukar Awwal ya na da halin kirki na daure na amshi ta yinsa, wata kila Allah ya d'auke Isa ne saboda rabon Awwal ce ni.
Da to na amsa mata na koma d'akina ina ta zubar hawaye.
Wata biyu masu zuwa aka saka ranar bikin yayyuna. Na yi murna sosai kuma na yi kuka kasancewar da Isa yana raye da yanzu har da bikin mu.
Dai-dai lokacin kuma mukayi walimar gama makarantar secondry school d'inmu. Munyi murna sosai ka sancewar muna daga cikin d'alibai masu hazaka da malamai suka yaba mana. Kuma muna daga cikin k'ungiyar MSS har ma ina a matsayin mataimakiyar Amira.
Lokacin auren su Aunty dija ya na ta gabatowa ana ta shirin biki, haka kuma daga bangaren Awwal ya na ta nacin zuwa. Ganin bai samu had'in kai a wurina ba sai ya koma ya aika manyan sa wurin baba a kan aba shi damar zuwa wurina. Lokacin da na ji haka na yi dariya sosai domin abin da ya kamata ya yi tun a farko ne bayyi ba sai yanzu. Haka Babanmu ya ba shi dama tilas idan yazo sai na fita na saurare shi har ya yi nasara na amshi soyayyar sa. Ko da ya samu haka tuni Babanmu ya ce matukar yana cikin shiri zai iya ba shi ni nan da sati takwas. Tuni Awwal ya amsa da babu wata matsala, don haka shirin biki sai ya zama na mu uku ake yi. Daga nawa sashen ba zan iya cewa ina farin ciki ba, kuma ba zan iya cewa ina bak'in ciki ba. Saboda a yanzu ina jin Awwal a zuciyata sosai. Sai dai duk da haka idan na tuna Isa sai na ji sam bana da muradin rayuwa da kowanne d'a na miji.
Haka su aunty suka yi ta yi min fad'a da kuma nuna min mahimmancin auren Awwal domin tunanin si zayyi wuya na samu me min irin wannan son. Tun da sun ga yadda ya na ce min duk da irin k'orar da na yi masa.
Wasa gaske har ranar aure ta zo, akayi duk wata hidima da ake yi a wurin aure aka kaimu gidajen mu. Abu mafi farin ciki iyayen mu da d'anginmu ba su da ra'ayin durawa amare magunguna na mata idan za'a kai mace gidan miji. Iya wuya kawai akwai wani had'i da innarmu ta yi mana ana gobe za'a kaimu ta bawa kowa ta ce take ya shanye ya bata kwanon.
Tun a daren farko na fuskanci Awwal yana da matsala, domin daren farko na kowacce

amarya da ango dare ne da ake sa ran farin ciki zai mamaya, domin dare ne na d'okin ango kuma na fargaba a wurin amarya. Tabbas na ga d'okin har ma da zalama a wurin Awwal, se de cikin wasu mintuna da badu wuce shida ba Awwal har ya gama cin amarcin sa ya baje yana bacci. Na yi mamaki matuk'a da jin yadda aje ruruta daren domin anawa b'angaren banji wata hangurb'ar damuwa ba. Hasalima zan iya cewa Awwal ba lalle ne idan ya cimma hak'arsa ba, tun da na san cikakkiyar budurwa na ke.

Wasa farin girki! Dare na biyu Awwal bai ma san da ni ba. Sai da muka d'auki tsawon kwana goma kafin Awwal ya kuma waiwaya ta, ranar sai da....Yi kuka da idanuna, saboda tamkar a jefaka a lilo za'ayi maka linji ka rufe idanu da niyyar jin dad'i kawai sai ka jika an gwara kanka da bangon da ke gefen lilon kuma an barka ba me lallashi bare kuma baka hakuri .

Na yi kukan zahiri har ma da kukan zuci. Amma kuma da matukar kunya na ce da Awwal ga matsala.

Bank'ado da kofar da ya yi shi ne ya saitani na dawo tsaf daga tunanin shekarun da suka shud'e. Fuska ba annuri na yi maza na mike na zuba masa abinci na wuce d'akina.
Wase gari tare muka fita amma kowa da motarsa, makarantar islamiyya na ya da zango.

Bayan karatun safe mun fira karyawa Adama ta bude mana jaka da tulin maganin mata har ma da maza. Kun san mata da kayan mata kowa sai ta fara jida har da masu d'aukar yajin maza. Ganin haka sai na ce da Adama ta had'amin kowanne guda bibbibu da na mazan da matan zan kai unguwar mu akwai me son siya. Farin ciki sosai adama ta yi ta had'amin ta bani na karb'a cikin zuciyats cike da farin ciki yau na samu makamin da zanyi nasara akan Awwal. Sai dai ashe da sauran rina a kaba............

9

Ina ta farin ciki a cikin zuciyata yau ni ma zanyi bacci me d'adin gaske. Domin na gama yanke hukuncin na samu maganin matsalata. Gida na koma daga makaranta na fara shirya mana abin da zamu ci. Kamar kullum dai zuwa k'arfe biyun rana na kammala komai. Yara suna gidan Hajiya Bonbino yau bai dawo da wuri ba. Ina tsaka da kallon tv ina sauraren wa'azi tukunna na ji zuwan sa a mota. Ban yi wani yunk'uri ba har ya iso bakin k'ofar falon. Ko da ya shigo daga inda na ke na yi masa sannu da zuwa gudun kar na yi wani abu ya ga ina rawar kai ne. "Yawwa." Ya ce da ni sannan na ta shi na amshi jakar sa na bi shi har d'akin na sa. Ko da muka shiga gefen hado na zauna na ce, "Wanka ko abinci wanne za ka fara?" Tare da turo baki gaba wai ni adole irin matar love d'innan. Jim kafin ya ce, "Wanka zan yi." Da to na ba shi amsa na wuce toilet na sa na na had'a masa ruwan wanka na fito. Ina fitowa na koma bakin gadon tare da fari da idanu na ce, "Masoyi, na had'a ruwan wanka sai gare ka."

Yi yayi kamar bai ji me na ce ba, sai kuma ya ce, "To ai sai ki je falo ki jirani zan cire kaya ne na saka jallabiya.". Murmushi na yi, idan da sabo na saba sa wannan kam. Don haka ban tanka ba na fice a bina a zuciyata kuwa na ce, " Hummm! Zamu had'e ne anjima za ka gane da wa kake magana."
Ban go na kaiwa harbin iska cike da farin ciki na wuce kitchen. Abincin sa na bud'e na d'auko wannan maganin da aka ce na maza ne na barbad'a masa shi sosai ta yadda zai buge shi yadda ya kamata. Ko da na je na ajjiye ina jiran fitowar sa amma shiru. Sai da na fidda rai da

fitowar sa sannan ya fito ya zauna na zuba masa ina yi ina satar kallon sa ina murmushi. Baki ya bud'e tare da bismillah ya fara a fawa cikin sa, har ya gama ba muyi magana da juna ba ni dai kawai na matsu na ga sakamako. Sauri na yi na shiga daga ciki na kuma gyara jikina da turaruka masu k'amshi saboda tsaro domin ban san ya abin zai kasan ce ba. Yanzu ne ko sai zuwa dare. Abu kamar wasa dai har yamma ba wani alamu a wurin Awwal na canji. Sai jikina ya yi sanyi duka ina kuma fatan Allah ya sa zuwa dare na ji alheri. Misalin tara na dare na wuce d'akina na kwanta ina saka rai da tsammanin kira daga gare shi idan magani ya fara aiki. Amma shiru har na fara jin bacci, kamar dai wasa baccin ya yi gaba dani sai da asuba na ji yana buga min k'ofa.
Ko da na farka ma ga lalle maganin nan bai masa komai ba kawai sai na fashe da kuka. Na jima ina yin kukan kafin na je na yi alwala. Sallah na yi na zauna ina lazimi har gari ya fara haske. Daga nan kuma na wuce madafa.
Takwas a makaranta ta yi min rai na duka a jagule
Adama ta dube ni, "Ke kuma Samha me ya sa me ki yau?"
"Me kika gani."
Na ba ta amsa.
"Kawai yau na ga ba kya walwala ne."
"Au to wannan ai ya na faruwa ga kowanne mutum, saboda wani lokaci ka ji kana walwala wani lokaci kuma ka ji ba son magana. Wannan kawai shi ne."
"Haka ne kam, to yanzu dai ina kayana su ke? Ko an siye?"
Dariya na yi ta dole da na tuna ba amfanin da maganin ya min, ciro su na fara yi a jakata ina ajjiye mata akan bencin da muke zaune. "Adama ba ta gari matar amma wata ta d'auki k'ulli guda na mazan ta ce na tambayo mata kud'in sa kuma wai ta ce ba shi da kyauma."
Na k'arashe maganar ina galla mata harar wasa.
Dariya Adama ta yi har da shewa tare da fad'in, "Haba wa! Ai kuwa dai maganin me kyau ne, sai dai idan shi mijin ne ba abin arzik'i a gare shi."
Kallon ta na yi da mamaki na ce , " Lalle Adama, to mene ne amfanin siyan maganin? Daman ba don a gyara ba ne?"
Dariya ta yi har da bugar cinyata ta ce, "Ke malama saurara na yi maki baya ni da kyau! Shi fa maganin mata da maza da ki ga gansu dukan su, Ana amfani da sune idan an d'an gaza ko kuma ka ji ka sauya daga yadda ka ke da, amma batun wai kana mara kuzari ka zama me kuzari d'ari bisa d'ari, to ba zayyu ba. Sai dai idan baka sa kuzari ya d'an taimake ka. Idan kuma kana da shi ne za ka k'ara sai ya hautsina ka har a arasa gane maka. Wanna shi ne. Ko kuma shi me son ya yi amfanin da magani ya zama ya gane wanda yake masa amfani sosai."
"Hummmm! Adama yau she kika san duka wad'annan bayanan?"
"Ke zauna can, dukkan sana'ar da zanyi sai na yi bincike a kanta."
" To yanzu dai ya kamata ki sayi ko guda ne saboda a gyarawa baban Ameera, ita kuwa wancen ki ce ta bayar da dubu guda."
Idanu na zaro da jin kalmar dubun da zan biya ta asara tun da ba wani abun da ya min maganin. Na ce, "Ke Adama yanzu wannan abin ne dubu? "
"Tabbas kuwa, don ma ta ce bai mata ba ne da har da d'ari biyar za ta biya."
"Cab! Lalle kam, zan kawo miki gobe idan na amso."
Na ba ta amsa. Turo min wasu kalolin zuma ta yi gaban tare da cewa lalle sai ma siya guda wai

tana da kyau idan  na siya zan samu alheri.
  Dariya kawai na yi na tura mata kayanta na sanar ma ba yanzu ba don tafiya zayyi ma shi yau zuwa damaturu.
Na sanar mata hakan ne kawai don ta barni da abin da yake damuna. Ina cikin wannan halin idan na ce zan sha wani abu kuma ai yau sai dai na tallata kaina, na fad'i hakan cikin zuciyata tare da istigfari.

Da yake Salma bata zo na ana ta shi na koma gida, sai dai ina shiga na tarar da wani abun mamaki.......

10

Ko da na shiga cikin falon tsayawa na yi cak! Sakamakon ganin mu'azzam zaune a falo shi kad'ai yana mun murmushi.Mamaki fal ya kama zuciyata
To shi kuma me yake yi ana shi kad'ai? Ban gama mamaki ba na ga Awwal ya fito a d'akin sa yana fad'in yawwa ga tanan ma ta dawo. Karfin halin na yi bayan mamakin ya gushe na shiga cikin falon ina k'ak'alo murmushi, zama na yi daga d'aya daga cikin kujerun ina fad'in, "Sannu da zuwa. Yau kai ne ka kawo mana ziyara?" Murmushi ya yi ya ce, "Eh fa ziyarar bazata mijinki ya jawo ni har ta tsawon sati guda. Dam! Na ji zuciyata ta harba da batun satin. Ina tsaka da tunanin Awwal ya dube ni ya ce, " Ki yi sauri ki shiga kitchen ki daura mana abin da zamu saka a cikin mu. "
Da to na amsa na gaida bak'on na wuce d'akina na cire kayan inifom d'in, atamfa riga da sket na saka sai na samu wani mayafi mai kauri na saka ta yadda ba zai bayyana jikina ba. Kitchen na wuce na barsu suna zaune suna hira. Sauri na yi na d'ora mata shinkafa da miya ta kayan d'anye wacce za ta ji nama. Cikin iko na ubangiji cikin miti arba'in tuni har na gama komai. Ina had'a kunun aya sai ya shigo kitchen d'in ya same ni tare da fad'in ban gama bane shi fa yunwa yake ji. Kallon sa na shagala da shi yadda ya min kyua kamar yau na fara ganin sa, Awwal ya cika na miji wanda Allah ya yi masa kyau da k'ira, ga kuma ilimi ga arziki. Amma sai dai kash! An rage shi da wata matsala babba wacce ita ce cikar jin dad'in ko wanne bawa. Jin ya kuma yin maganar duka sai ya saka min kasala a jikina har na ke jin kamar na je na rungume shi. Kallon sa na yi cikin yanayin da ba zan iya tantancewa ba tare da kashe masa murya cikin wani irin salo me wuyar fassara na ce, "Bombino, don Allah kar ka bari soyayar ka ta yi min illah a zuciyata, wallahi ina jinka a zuciyata sosai. Ina fad'ar haka wata kwalla ta cika min idanu ganin ko motsi bayyi ba. Ji na yi kamar ya ba ni wata dama ce hakan ya sa na je na rungume shi ko zan ji salama a cikin zuciyata. Kasak'ai ya yi yana jina bai ce komai ba kuma bai motsa ba bare ya rungume ni da hannnayan sa. Jin na saka hannayena bisa kansa ne ya sa ya fara ja da baya yana kok'arin raba ni da jikinsa. A daidai wannan lokacin kuma na ji muryar mu'azzam yana fad'in, kun shanyani da yunwa kun zauna soyayya ko? Jin sautin sa tuni Awwal ya yi fatali da ni gefe ya fice. Wata irin kunya da nadamar abin da na aikata suka rufe ne, domin irin haka bana sanin na aikata sai bayan faruwar abun, kuma hakan ya samo asaline daga yanayin da nake ciki game da shi.  Kayan na fara fita da shi zuwa falo ina ta sun kuyar da kaina kasa kamar munafuka har na had'a komai na jere a dining. Dukan mu sallah mukayi sannan na yi wanka na

kuma shiryawa muka hallara a teburin cin abinci. Muna zaune bayan na zubawa kowa muna ci shi sarkin kunya kansa k'asa ba ya ko dagowa yana yiwa mu'azzam zance, ya yin da shi kuma mu'azzam duka hankalin sa akaina yake yana ta satar kallona. Ni kuwa yau ban tsinci kaina da jin haushin sa ba, saboda ko wacce mace burin ta mijin ta ya kalle ta idan ta yi ado, amma shi ya duk'ufar da kai kamar me tasbihi shi kuwa yana kalle masa. Har muka kammala cin abincin nan bai d'ago da idanun sa ya dube ni ba. Don haka nima fa gaba d'aya nutsuwata ta koma kan mu'azzam har na fara maida masa da martanin murmushin. Bayan mun kammala na koma d'akina sai kuma na ji ban kyauta ba sai na fara istigfari ina neman yafiyar Allah. Jin shigowar sa bai sa na kalle shi ba domin na san shi ne da ikon zuwa a wannan lokacin. Kallona ya yi sau d'aya da na d'ago ya sauke ya ce da ni, hajiya ta yi tafiya ta sati guda kuma ba zai iya barin mu'azzam da ba shi da mace ba tare da k'anwar sa wacce ba aure a gida ba hakan akwai hatsari. Don haka mu'azzam zai zauna anan tsawon sati kuma baya son zaman hira ko da baya gida iya ka ta da shi kawai gaisuwa da ba shi abinci a duk lokacin da ya bukaci hakan. Mamaki ya kamani sosai da jin wai da gaske satin zayyi. Lalle Awwal zai kawo mana damuwa cikin zaman mu wacce ta fi ta baya yawa. Domin da zaman sa gidan nan gwanda can, tun da ba su san ya abin yake ba . ta ya zai kawo min k'ato gida bayan ya san ba iya min ya ke ba kuma ya ce mu zauna haka kawai. Jin na yi shuru ina tunani a zuciyata ya sa shi cewa, "Dake na ke fa." Kai na d'ago na dube shi na ce, "In sha Allah."

Da ga haka ya juya ya fice a d'akin. Ban kuma fitowa ba sai da na yi sallar la'asar kafin nan na fito zan d'aura girkin. Ina fitowa na wuce kitchen sai na ji kamar motsi a falo sai na juya, Mu'azzam ne zaune yana ta aikin kallon film d'in labarina maimai ci na su sumayya da fresido. Da sauri na wuce shi domin bai ganni ba. Aiki na ke tuk'uru ina son na gama da wuri domin ina da wani program na da k'awayena a wasaf da zanyi. Karfe biyar dai-dai. Ji na yi kamar motsin mutum, ko da na juya mu'azzam ne ya tsaya yana k'are min kallo. Dam! Na ji zuciyata ta harba, "Wannan kuwa ya san me yake yi?" Na furta a zuciyata. Sosa kai ya yi ya ce, "Ase dai kina kitchen d'in, ina zaton ma ko kina bacci ne shi ne na ce bari na d'aura shayi saboda ni ma'abocin shan sa ne sosai. To dunda kina nan kya dafa min idan kin gama.

Sai da ya k'arkare da batun sanna na ce masa, " Okay ba damuwa zan had'a maka."

Da to ya amsa tare da juyawa ya fita. Bayan na gama da na fito baya falo don haka sai na yi sauri na zauna a falo na d'auki wayata domin ba na so su fara bana kusa. Ina hawa kuwa am fara da gabatarwa, don haka duka hankali na ya tattara akan wayar. Ji na yi kamar an tsaya a kaina, don haka sai na juya na ga ya sake mun murmushi, "Wai matar me kika samu ne a waya ina ta sallama baki san ma ina yi ba." Ya tambaye ni cikin shagwab'e fuska. Na bude baki da nufin ba shi amsa kawai sai na ji motsin bude k'ofar falo, ko da na juya Awwal ne ya shigo.Kai tsaye bai ko kalle mu ba mu'azzam yana fad'in har ka iso ke nan, bai amsa ba kai kawai ya gyad'a yawu ce, ganin haka tuni ni ma na koma d'akina. Ko a wajen cin abinci su na zubawa ni kuwa d'aki na tafi na ci na wa a can. Sai wajen goma na dare Awwal ya min tex yana nema na a d'akin sa. Shiryawa na yi na tafi zuciyata tana ta taradadin abin da zai ce. Ko da na je ya jima bai kula ni ba har sai da na gundura da zaman kafin ya ce, "Yau yau na saka doka har kin fara karyata? Wai baki lura mu'azzam yayi rayuwa a turai ba ne? Shi shigewa mace ba komai ba ne a wurin sa , amma duk da haka ba zan iya jurar irin haka ba. In kin sa ba zaki kiyaye dokata ta daga yau zaki na wuni gidanku har sai ya tafi."

Kallon sa na yi na ce, "Kai ne fa ka kawo shi, kuma shi ya shigo falo ya same ni ba ni ba.

Idan har ba baka yarda da kanka ba na mene ne ma kishin? Ai ina ganin abin da kake so shi za kai wa kishi."

"Samha! Ya k'irani cikin wani irin yanayi na b'acin rai. Kallon sa na yi tare da rike masa hannu domin na san masifa ce zayyi na ce, " Don Allah ka bar wannan zancen da za kai, ka fuskanci matsalar mu ita ce abin dubawa ba wai wani batu da kai da kanka ka kawo shi ba. Ba ni da burin da ya wuce a ce yau ka zama cikakken na miji."

Kallona ya yi ya kasa ce min komai, na d'ora da cewa, "Ta ya zaka kawo min wani gardi cikin gida ka ce mu zauna tare da shi bayan ka san matsalarmu Awwal?"

Ka sa ko da motsin kirki ya yi ya sunkuyar da kansa sannan ya ce, "Samha fita min a dakina......

11

Shuru na yi ina ganin yadda yake dad'a matse idanun sa gan baya son ya bud'e su. Fita kawai na yi tare da fad'in, "Ina dai sa ke tuna maka." Daga haka na fice zuwa d'akina. Shi kuwa Awwal a b'angaren sa ya na jin ta fita ya bude idanun sa tare da cewa, "Oh Allah Samha ta fitsare ba ta jin kunyata sam! " Gadon sa ya haye yana na zarin kalaman ta tare da jin haushin sabon halin da ta zo masa da shin

San da ya auri Samha yarinya d'anya sharaf da ita bata san komai ba shi ya koya mata komai, amma yau wai shi take ikirarin baya isarta? Ko da ya fad'i maganar sai da ya kuma kulle idanunsa, domin lamarin kunya ya ke ba shi matuk'a. Wanka ya shiga ya yi, bayan ya fito ya zauna abakin gadon yana latsa waya cikin intanet ya kutsa yana nazarin halayyar mata wai a tunanin sa ko a kwai wani hali da mata suke da shi ne wanda Samha ta gani ta d'auko bai sani ba. Amma har ya gama bai ga wasu daban ba. Ganin zaman ba shi da amfani ya sa ya haura gadon sa ya kwanta, can kuma sai wani tunani ya zo masa, yadda Samha ta raina k'ok'arin sa ya kamata ya nuna mata shi fa ba lalatacce ba ne. Da wannan tunani ya cire kunya ya wuce d'akinta. Ita kuwa baiwar Allah tuni har bacci ya fara d'aukarta cike da mafarkan da ta saba. Ji ta yi ana jan yatsun k'afarta kamar a mafarki kamar a zahiri. Farkawa ta yi ta gansa tsaye a kanta. Don haka cikin mamaki ta ta shi zaune. Domin ta ya jima bai zo d'akinta ba sai dai ta je wurin sa. Kafin ta yi magana ya hayr gadon ya juya mata baya tare da lumshe idanunsa. Ganin haka tuni ta ji wani sanyi a ranta ta san ya zo ne ya bata hakkin ta. Baya ta juya ita ma domin ta amshi sak'on da zai bayar. Jin sa a bayanta ya rungume ta hakan ya sanyata farin ciki sosai da zak'uwa da yanayin. Wasa gaske dai Samga yau ta tsinci kanta cikin yanayi na jin d'adin abin da Awwal yake mata. Sai dai kash! Ana zuwa inda ta fi so da k'auna fa ya jibgemata yana numfarfashi. Domin ji yake a wurin sa ya yi babbar bajinta. Wasu siraran hawaye ne suka fara safa da marwa a fuskarta tare da fad'in, "Awwal mene ne kuma haka? Don Allah ka ci gaba, wallahi zan iya mutuwa yau kam idan baka ba ni farin ciki ba."

Jin batun ta ba k'aramin mamaki ya ba shi ba. "Samha yanzu dukkan wannan k'okarin da na yi har yanzu ban rufe bakin ki ba? Yadda na bawa kaina wahala domin rufe miki ba ki da kuma sanya ki farin ciki a she banyi ba? To wallahi ina baki shawara tun wuri idan ma wasu suke zuga ki kina shan wasu abu domin ki k'ure mijinki to ki daina. Kuma ki sani wallahi ba zan kuma iya wani abu haka kawai gobe na ka sa fita ba."

Yana gama fad'ar hakan ya fi ce a d'akin ya bar Samha cikin matsanancin hali. Birgima take

iya birgima har ta wantsalo a kan gado tana cikin damuwa bata sani ba.
Jin ta bugu da bangon d'akin ya sanya ta dafe wurin tare sa saurin mik'ewa ta koma gadon tana dafe mara tana hawaye. Ganin zaman bazayyi ba ya sa ta fita tana dafe bango domin ta je kitchen ta duba lemon tsami ta sha ko za ta samu sauk'i. Duhu duhu take gani  da yake idanun ta tsabar wahala ba ta iya bud'esu sosai. Tana shiga tana lalume ta ji ta lalumi mutum dai'dai marar sa. Jin abin ba irin na su ba shi ne ya sanyata d'an k'ara bude idanunta kad'an tare da lumshe su. Ita da 'yarmaye ba maraba. Shi kuwa Mu'azzam yana kwance yaji marar sa ta dame shi da damuwa don haka ya san dai ba za'a rasa kayan shayi ba. Kuma daman ya sa ba tun a gidan su kullum abin ya dame shi haka ya ke fita ya had'a kayan sa ya sha ya samu sauk'i. Jin an dafa wajen har sai dai ya ji yana shirin sumewa. Domin abu ne da bai tab'a ji ko aikatawa ba. Sake jigbe masa ta yi tare sa rungume shi tsaf a jikinta tana fad'in, "Me kake yi kuma anan Awwal? Wallahi Awwal yau idan na mutu tabbas kai ne sanadi."
  Jin ya yi shuru bai dame ta ba domin ta san halin sa ne. Amma abu mafi firgitarwa shi ne da ya sa ta ja da baya da shi shi ne............

12

Jin wani irin kamshin turare wanda ba na shi ba shi ne ya sanya ta ta ja baya da ga jikin sa. Idanu ta kuma warewa sosai tana kallon sa domin tana son ta gane shi. Shi kuwa Mu'azzam ga ba d'aya ta sincema sa notin kai da na jiki kuma duk ta rikita shi. Ganin Mu'azzam ne tsaye gabanta tuni ta ja da baya. Yunkurin ta na son fita akitchen d'in ya k'i samuwa don haka sai ta koma can gefe da shi ta zube tana lumfarfashi . Shi kuwa ganin haka gaba d'aya sai ya rasa abin yi. Fita ya yi a kitchen d'in ya nufi bakin d'akin Awwal zai buga masa kuma sai ya fasa. Wani tunani ya yi ya sa shi tsyawar. Domin ya fahimci matsalar ta. Kuma yana tsoran kar Awwal ya zargi wani abu game da shi. Don haka sai ya wuce d'akin da aka ba shi bakinsa akelum ya zauna bakin gadon sa. Mamaki yake sosai, daman ana iya samun haka a zaman aure mace har tana kuka da neman taimakon mijinta amma mijin ya gaza yin hakan? Shi kuwa Awwal wane irin mutum ne haka? Ko dai wani mummunan lefi Samha ta yi masa wanda bai sani ba? Ganin ba shi da mai ba shi amsar duka tambayar ta sa ya sa ya kwanta yana juyi da damuwar da yake ciki ga shi ko shayin bai samu had'awa ba wannan matar ta kuma k'ara masa damuwa.
  Alwala ya yi ya fara sallaoli ko zai samu nutsuwa da jin sauki a ziciyar sa. Samha kuwa kusan awa guda kafin ta d'an samu sukuni ta koma d'akinta. Bacci ne me nauyi yayi nasarar d'aukarta sosai wanda ya sa har ta makara bata yi salla ba. Ko da ta farka sai take jin kamar mafarki nd ba zahiri ba.
Sassafe Samha ta rasa gane kanta sam, me za tayi yanzu. Ta ya zata iya bud'e idanu ta kalli Mu'azzam idan har abunnan a zahiri ne ba a mafarki ba? Ganin ba ta da mafita sai Allah ya sa kawai ta shirya kayanta wanda zai kaita kwanakin da Mu'azzam zayyi agidan ta sulale ta bar gidan ko abinci ba ta dafa ba. Dirar mikiya ta yiwa gidansu wansa hakan ya sa mama tambayar lafiya kuwa. Kuka ta saka tare da cewa "Mama har yanzu fa Aljanunnan suna gidan Awwal."
  Idanu Mama ta zaro tare da fad'in, "Ke Samha ki rufawa kanki asiri a rayuwa Wallahi, ina

rabaki da kiyon akuya kina ga kyalla ta haihu.." Zumb'ura baki Samha ta yi ta wuce d'akin mama bata ce komai ba.

A can gidan Awwal kuwa yana kwance shuru har wajen tara baiji motsin kowa a falo ba, kuma Samha ba shigi ta gaida shi kamar yadda ta saba ba. Don haka sai ya yunk'ura ya fito falo ya zo ya ga bata nan, kai tsaye kitchen ya wuce nan ma wayam. Tunawa da yayi da rigimar jiya da dare sai ya nufi d'akinta nan ma ba ta nan. Mamaki sosai abin ya ba shi. To ina ta tafi a wannan safiyar ya tambayi kansa.

Wuri ya samu ya zauna akan kujerar falo bayan ya fito a d'akin ya fara gwada lambarta tana shiga amma bata d'auka. Hankalin sa ya yi matuk'ar ta shi da jin hakan. Tagumi ya yi yana nazarin abin yi sai ga Mu'azzam ya fito a d'akin sa, wuri ya samu shi ma ya zauna suka gaisa sannan Mu'azzam ya dube shi sosai cikin kulawa ya ce, "Me yake faruwa ne haka?"

"Me ka gani?" Awwal ya maida masa da tambaya maimakon amsa. "Aa na ga ka yi zaman tagumi ne." "Aa babu komai kawai dai wallahi Samha ce ban gani ba duka gidan, kuma na k'ira layinta ba ta d'agawa."

"Oh Samha ai tun sassafe na ga fitarta na zaci ma tare kuka fita fa."

"Fita kuma?" Awwal ya tambaya.

"Tabbas! Amma me ya faru. Sanar min na sani."

"Babu komai ni ma ban sani ba." "Haba Awwal taya zaka ce baka sani ba, kai ne babba fa Awwal. Kuma jiya na ga Samha a cikin wani yanayi na jinya, kuma na ji tana ambatar sunan ka."

Kai Awwal ya d'aga a fusace ya ce, "Mu'azzam! Me ka ji tana cewa? Sannan kuma me ka fito yi kai a wannan lokacin?"

Sosai kai Mu'azzam ya yi tare da fad'in, "Ni kuma taya zan san abin sa take fad'a, na fito ne ina kitchen ina had'a magani kuma kasan dai halin da nake ciki. Dole ma na yi aure na huta." Mu'azzam ya fad'a yana tsaki tare da juya kansa gefe. Tsakin shi ma Awwal yayi yace, "Banza mayen mata kawai, wannan dalilin ne ya sa ba zan bari ma Salma ta san kana sonta ba. Bare kuma ka aure ta."

Dariya sosai ya kyalkyala da ita, "Haba kai kuwu ai asara ce zaka yi mata wallahi. Domin matan yanzu fa ba sa son auren mata maza, gwanda dai ka ba ni sai kuji mu shuru. Amma idan ka aura mata wanda yake maza ya rako ko, to tabbas kullum cikin fitina zasu zauna."

Dum! Ya ji da maganar Mu'azzam, domin ji yayi kamar da shi yake. Duk da dai shi ya san ba ya da ga cikin mazajen sa Mu'azzam yake nufi.

Mik'ewa ya yi tare da cewa, adai bi wani sarkin amma ban da wannan. Ni zanje na nemo matata kayi mana kirki tunda ka iya daman." Dariya Mu'azzam ya yi ya ce wannan ba matsala ba ce, kai de ka je ka nemo mana matar tun kan dare ya maka kuma ka bata hak'uri tabbas na san ka yi mata laifi. Don da gani zata yi hakuri wallahi."

Awwal dai bai ce komai ba ya wuce d'akin sa yana kuma maimata k'iran layin Samha. Ganin dai ba zata d'aga ba kawai sai ya shirya ya d'auki mota lokacin kuma Mu'azzam ya shiga ya fara girka musu abin da za su ci."

Har k'ofar gidan su Samha ya faka motarsa sannan ya shiga daga zaure yayi sallama aka ba shi damar shiga. Bayan mama ta ba shi damar zama ya zauna sun gaisa ya ke tambayar ta ko Samha ta zo? Ta ba shi amsa tana nan. Hakuri ya fara bawa mama akan cewa bai san ta fito ba. Mama tace karya damu yanzu zata fito su tafi. Mama ta kwalawa Samha k'ira Samha ta fito

sanye da hijabi amma ta na ganin Awwal sai ta fasa ihu ta zube a wurin irin dai yadda take yi alokacin da Awwal yayi mata wasan aljani.......... Tofa an yanka ta tashi.

13

Da sauri shi da mama sukayi kanta, jijjiga ta mama take yi sosai. Awwal kuwa ruwa ya d'ebo na fara yayyafa mata. Idanun ta ta bude tana ganin sa ta yunk'ura ta fara ja da baya tana fad'in, "Mama karki yadda da shi ba Awwal ba ne aljanine, zai cutar dake. Awwal ba ya murmushin nan.
Kallon sa mama ta yi ta ce, " Wai me yake faruwa ne? Aljanun ne ko kuma tsora kawai take yi."
 Sun kuyar da kai Awwal yayi sannan ya ce, "Mama shi ne abin da na gaza ganewa. Addu'a sosai mama ta fara yi mata tana gyara mata zaman, amma sam Samha ta k'i amincewa ta kuma ko sa kallon Awwal. Har mama ta fita a d'akin ta barsu tare. Awwal ya dube ta yace, " Samha, don Allah ki ta shi mutafi gida, wallahi ba wani aljanin a gidannan kawai ki tsorata ne tun baya."
 "Ba zan koma ba sai sanda zuciyata ta tabbatar da hakan tukunna. Ka bar wurinnan kafin ka sanya ni cikin masifa."
 Ganin babu sarki sai Allah ya sa Awwal yiwa mama sallama ya tafi. Ko da ya koma Mu'azzam ya na zaune a falo ya gama had'a komai da za su karya yana jiran dawowar sa.
 Da ya kalle shi shi d'aya ya tambaye shi ina Samhan take ne. Bai amsa ba sai da ya samu wuri ya zauna sannan ya ce, "Tana gidansu, kuma ta ce ba zata dawo ba."
 "Tofa akan me ya sa to?" Mu'azzam ya tambaya. "Wani shiririta ta ke ji da shi. Wai ba zata dawo ba gidan akwai aljani." Dariya sosai Mu'azzam ya yi ya dubi Awwal, "Aljani kuma? To kai kuma sai ka barta ta zauna. Gaskiya ka lallab'ata ta dawo dan dai gaskiya ina jin kawai dan karta dawo ta ce maka haka. Wata k'ila kayi mata wani laifi ne ba zata iya sanar maka ba shi ne ta fake da aljanu."
 "Ai kuwa za ta ga aljanu, domin ba zan je na dawo da ita ba. Ko wanne irin lefi ne ai ya kamata ta sanar min ba wai ta tsaya shirme ba. Kuma ma ba wani laifi da na yi mata ni a yanzu. Don haka na huta ma ta sha zaman ta.
 " Aa fa Awwal karka maida kanka gauron k'arfi da yaji a kan abin da bai kai ya ka ba, ya kamata kaje ku sulhunta." "Sai ka yi ta yi kai wannan ya dama ni bani da damuwa. Daga haka ya ta fi ya fara zuba abinci. Ganin haka ya sa shi ka Mu'azzam ya bi bayan sa ya zuba na shi. Suna ci suna hirar su ta abokai har suka kammala. Fice wa suka yi duka agidan, agidan Hajiya suka ya da zango. Salma ce ta gaida su dukan su sannan yaran suka gaishe su salma ta tambaye shi yau she zai d'auki su Ameera za ta fita anjima da yamma. Sanar mata yayi anan zasu zauna har zuwa sanda mamar su zata dawo ita ma ta yi tafiya. Shi dai Mu'azzam bai ce komai ba da jin k'aryar da ya mata.
 Samha zaune a bakin gadon mama tana nazari da tunani har su aunty dija suka zo gidan yini. Ganinya ya sa suka yi farin ciki da zuwan na su saboda sun jima ba su had'u a gida ba sai dai kowa yayi zuwan sa daban. A lokacin da suka san dalilin zuwan ta sai kuma suka ka yi mata nasiha da fad'a akan ta dage da karatun Alkur'ani kuma ta cire komai azuciyarya na batun jinnu.

Da to ta amsa musu amma ta ce suyi mata uzuri ta samu nutsuwa nan da wasu kwana ki sai ta koma. Amma a yanzu ba ta da nutsuwa. Ba su takurata ba suka barta da abin da ta ce d'in. Sai dai sun sanar mata duk yadda za'ayi kar ta bari su baba da yaya Yusuf su dawo daga tafiya bata koma ba.

Wasa gaske kwanan Samha uku bata gidan. Gaba d'aya hankalin Awwal ya fara ta shi da rashin ta agidan. Tun da sukayi aure bat tab'a tafiyar ko da kwana d'aya ba. Duk da cewa wuri kwanciyar su ba guda ba amma sam idan dare yayi sai ya shiga damuwa. Yau ma yana kwance a falo shi da Mu'azzam suna hira ya ce masa zai je ya kwanta. Ko da ya shiga d'akin sa wayarta ya fara k'ira, kamar ba zata d'auka tukunna ta d'auka. Gaisawa su ka yi sanna ya tambayeta yau she zata dawo. Amsa guda ta bashi wacce ta sany shi mamaki, wai sai ranar sa ya can ja hali kuma ya samu lafiya.

Wannan maganr ta jima tana masa yawo a ransa. Wane hali ne da shi wanda zai sauya shi? Kuma kenan har yanzu tana jin cewa shi ba mai lafiya ba ne? Ba don yana sonta ba da tabbas zai saketa ta auri masu lafiyar da take buri. Sai dai ba zai iya tab'a sakinta ba. Kuma shi ya san yana daga cikin maza masu lafiya, amma matan yanzu sam sun damu kamsu da cewa sai na miji ya sha wani abu na magani sannan zai iya musu, suna so sai sun ga na miji ya fita hayyacin sa sannan za suyi farin ciki. Ko kuma sai yana zunduma ihu irin yadda masu magunguna suke yad'awa. Humm aikuwa Allah ya kiyaye shi da wannan aikin. Ba zai tab'a shan wani abu domin ya birge mace ba, tunda dai ya san yana da lafiya ga shi har ya haifi yara uku. Lafitar da Allah ya bashi tunda har ta kai ya ba ta ciki ta haifa ai renin hankali ne ma ta ce wai z ta gamsuwa da shi. Amma zai d'auki mataki akan hakan. Zai bincika komai na d'akinta ya kwashe magungunan da take sha ya watsar kuma ya mata gargadi na musamman. Da wannan tunanin ya tafi d'akinta har kuma lokacin Mu'azzam yana falo yana kallon bal, shiga ya yi ya fara bincike. Sai dai har ya gama bai samu komai ba. Murmushi ya yi tare da fad'in "Mata sun san munafurci ai ba zata barsu inda zan gani ba.

Hakura yayi ya koma ya kwanta. Ganin da gaske Samha ta k'i dawowa ya sa ya koma gidan amma yana zuwa ta kuma birkice masa tana ik'irari aljani. Abin ya b'ata masa rai sosai amma ba yadda zaiyyi. Dole ne ma ya lallab'ata kamar yadda Mu'azzam ya fa'da. Domin yana da bukatar ta sosai. Zama yayi daga ita sai shi a d'akin ya sanar mata cewa ya sauya saboda ba na da ba ne shi d'in, kuma in sha Allah za ta yi farin ciki sosai. Allah sarki abin ka da mai buk'atar hakan tuni Samha ta yarda da roman bakan da yayi mata. Bayan ya fita ta sanar da mama za ta koma. Mama ta yi dariya ta ce Allah ya kiyaye hanya. Kunya kuma duka sai ta lullub'eta.

Gidan suka dawo ta shiga kitchen ta shirya masu abincin dare. Shi kuwa Awwal sai fara'a yake yana ta kaiwa da kawo wa yana mata hira. Dare na yi yaje ya siyo musu nama me laushi wanda yaji yaji me dad'i tare da kayan sanyin. Samha aka canjad'a ado na musamma saboda yau tana cikin farin ciki mijinta ya fahimci matsalar sa har ma ya canja yace mata. Abinci suke ci suna hira kai ka ce wasu daban ne ba su ba. Ba za ka d'auka wannan Awwal d'in bane.

Mu'azzam ne ya shigo ua same su ya gaishe da su, amma ganin yadda Samha take jin kunyarsa sosai ya sa bai mata magana ba balle ya zolayeta yadda ya sa ba. Kai tsaye ya wuce d'akin sa domin ya barsu su sake. Bayan sun gama komai Awwal ya shiga ya fesa wanka ya wuce filin gida ya far motsa jiki, wai saboda ya samu jikin sa ya ware ta yadda zai nuna wa Samha ainahin k'arfin da Allah ya masa. Bayan ya gama ya samu kankana ya fasa guda ya

shanye domin a tunanin sa ita ma zata inganta masa lafiya saboda magani ce sa ya yarsa da ita d'ari bisa d'ari. Samha kuwa an sha kayan bacci an sha turaruka ana jiran aji shigowar Awwa falo. Domin ta ji fitar sa wajen gida, don haka da zarar ya wuce d'akinsa zata bi shi. Kwatsam sai ga shi ya shigo d'akin yana washe baki ya zauna bakin gadon tare da fad'in, "Baki yi bacci ba a she."

Mamaki fal ya kama zuciyar Samha bacci kuma wanne iri. Hayewa gadon yayi ya kwanta ya juya baya tare da fad'in, "Ina jiranki." Mamaki ya kama Samha, lalle Awwal ya sauya yau shine har sa yana jira? Cab! Lalle yau akwai sauyi tabbas. Hawa gadon ta yi ta kwanta tana jiran jiran da sai da ta yi nadamar yin sa..........

14

Kamar a mafarki take jin yanayin sa ya sauya irin na da, sai dai kuma ba ta ji yana munshari ba. Hakan ne ya sa take jin kawai ta tsorata ne amma ba wai ya gama bane. Jin nauyin sa ba k'aramin tayar mata hankali yayi ba. Ja da baya ta yi ta gyra kwanciya ta k'are masa kallo yadda yake fidda lumfashi kamar an d'aura masa wani nannauyan dutse. "Awwal wannan shi ne sauyawar da ka ce min?" Samha ta furta cikin wani rikitaccen yanayi. Sa ke matse idanun sa ya yi ya ce, "Innalillahi! Samha wai kina nufin har yanzu dai shuru ne....?"

Kuka ta fashe da shi sosai har ta na d'aga murya, "Wallahi Awwal yau kam wallahi Allah ya isa zan maka na rantse idan har ka ce min iya ka abin da zaka iya kenan.

Cike da ta shin hankali ya ta shi ua zauna yana fad'in, " Samha, don Allah karki min wallahi na kai k'arshe ban san me kike so na yi ba wanda ya zarce haka. Ina jin dai marsalar nan ke kina da ga cikin sahun mata ta fannin wannan lamari mataki na k'arshe. Amma don Allah kiyi hak'uri ki kwanta zuwa anjima zan dan yi bacci idan na farka sai ayi wani abu."

"Wallahi baka isa ba! Abun ma har da raina min hankali! Kana farke ma yaya bare kuma ka yi bacci. Wallahi Awwal na gaji tunda na karanta maka da yaran hausa na yi maka da boko yanzu kuma na yi maka da larabci amma sam ka k'i yarda, to ka wai ka sawwak'e mun kowa ya kama gaban sa Allah ya had'a kowa da alheri."

Ko da jin wannan batun na ta sai Awaal ya zaro idanu yana fad'in, "Haba Samha yanzu sai ki iya rabuwa da mijinki ki watsa farin cikin yaran ki saboda kawai wani abu da yake zuciyarki?"

"Tabbas Awwal, wannan shi ne abu mafi sauki da zanyi domin na ceto rayuwata daha halaka! Zama da kai tabbas halaka ce zallah. Yara kuma Allah ya raya mun su."

"Haba, ta ya zaman zai zama halaka me na rage shi da ke. Komai ina miki ko da kij fita ba lalle ki auri wanda zai baki gata irin wanda na baki ba."

"Na sani, baka rage ni da komai ba. Amma fa ka gaza ba ni farin ciki a gidanka. Na sani Awwal ko da na fita ba lalle na samu na miji da yayi min gata kamar ka ba. Ko kuma wanda zai inganta rayuwata kamar yadda ka min ba. Ko wanda zai girmama iyayena kamar yadda ka girmama su ba. To amma ka sani dukkan wannan abin da kayi min matukar ba zaka iya ketarar dani daga wutar Allah ba basu da amfani a gare ni ranar lahira. Gwanda mu rabu na koma gida na auri talakan da zai nemo mana cin yanzu ya nemo na ajima. Abun so shine ya zama min katanga

daga wutar da Allah ya tanadar wa dukkan matan da suka kasan ce mage da wuri a gidan aure.

" Cab! Samha ki sauya tunani wallahi ki nutsu ki yi hakuri dani in sha Allah zan sauya zakiyi farin ciki sosai da sosoi a rayuwar da zamuyi gaba."

"Sauyawa fa ka ce min Awwal. Shin har akwai wata sauyawa wacce zaka yi wacce ban sani ba? Ba ga irin sauyawar ta ka ba. Ina gida ina zamana ka je ka dawo dani ka ce ka sauya, amam kuma sai ga irin abin bak'in cikin da ka kuma shuka min. Ni dai na sanar maka iya gaskiya ya ne wallahi. Domin na lura ba zaka tab'a sauyawa ba. Haka Allah ya halicce ka don haka sai ka sama mana sauki. "

"Na san har kullum ba kya iya fahimtata Samha ke dai maganar ki guda d'aya yace wallahi ko da yause akan wannan za'a tsaya ake jin kanmu da ke? Ke yanzu wannan ba abin kunya bane a gareki a ce shi ne silar mutuwar auren ki?

" Tambayata kake? Wai tambayata kake wa zai aure ni? Bari ka ji duniya tana fad'i kuma Allah ya san cewa domin gudun sab'a masa na ke dukkan wannan abun. Baya ga haka da ba abin da zai sa na ce zan rabu da kai. Awwal wallahi ina sonka! Son da ba zan iya misaltamaka ba, ni nasan irin wahalar da zan sha a lokacin da zan raba kaina da kai. Sai dai ka sani yin hakan tabbas shine mafi alheri a gare ni da yaran nawa ma gaba d'aya. Domin ko su yaran nawa ba zasu so yau a ce ga uwarsu tana aikata wani abu mafi muni ba, ko kuma a koma ga Allah suka an yi min hisabi zuwa ga wuta.   Yaran nan uku ne fa, ka san inda zaka kai su ai ba sai ma sanar maka ba. Don haka kawai kayi abin da na ce maka kawai shi ne mafi sauk'i. Domin babu wani uzuri da zan yi maka anan gaba. In sha Allah zaka smau daidai kai ka aura . ni ma kuma Allah ba zai barni  haka ba tun da ba butulci na yi ba. Sai ba tabbata na yi akan bauta masa. Kuma ya bamu damar yin haka a lokacin da irin wannan  matsalar ta faru."

Lumshe idanu sosai Awwal yayi yana jin dukkan abin da Samha take fad'i, wani irin b'acin rai yake ziyarta zuciyar sa wanda bai san ma me zayyi ya huta ba. Shi kam baya jin zai iya rabuwa da Samha, kuma ya san ba zai iya abinda take so ba. To yanzu ina mafita cikin wannan lamarin na sa.  Ajiyar zuciya ya sauk'e ya sauk'a a kan gadon ya wuce bayin da ke cikin d'akin yayi wanka tare da alwala ya fito ua hau sallaya ya fara shirin tayar da sallah. Jin fad'uwar abu abayan sa ya sa shi da katar da sallar. Juyawa yayi. "Innalillahi wa'inna 'ilaihirraj'un." Shi ne abin da ya furta.

Ganinta zube kamar sumammiya shi ne abin da ya tayar masa da hankali. Gefe guda kuma haushinta ya kama shi saboda a ganin sa wannan 'yar matsalar ba wata matsala ba ce da zata sa kanta cikin damuwa har ta yanke jiki ta fad'i. Jijjigata ya yi shiru. Ganin haka sai ya koma bayin ya samo ruwa ya fesa mata sai ta kawo lumfashi. Kallonta yayi cike da b'acin rai ya ce, "Wallahi Samha abin nan ya ishe ni sam! Taya zaki zo kina tayar min da hankali akan wannan abin."

Lumshe idanu ta yi ba ta ce komai ba ta yunk'ura ta hai gadon ta kwanta ta yi lamo kamar me bacci. Ganin ta yi haka shi ma bai sake ce mata komai ba ya wuce ya kwanta. Ko da asuba ta yi ta yi wanka ta yi sallah ba ta kuma yi masa magana ba ta fi ce, ta yanke shawarar fita cikin sabgarsa kawai tun da ta lura sam ba zai tab'a fahintar ta ba.

Idan ta kawo masa abinci sai ta ajjiye a dining ta koma d'akinta. Haka idan dare yayi baya tarar da ita a falo ta ajjiye masa komai ta shiga har ta rufe ita da yaranta. Shi ma Mu'azzam ya jima rabon da yanga har yake tambayar Awwal ko ta kuma koma wane, amma ya tabbatar masa tana nan. Sai ana gobe zai koma gidan hajiya sannan suka had'u suka gaisa . washe gari da

yamma ya tattara kayan sa ya koma gidan hajiya saboda yau ta dawo daga tafiya.  Ita ma Samhan da washe garin ranar taje ta yi mata sannu da dawowa. Ko da dare yayi Awwal ya zo ya d'auketa yana tambayarta ko suje gidan abinci na Arraudah su ci abinci ne yaga kamar bata ci komai ba. Ban za ta ta yi masa bata ba shi amsaba har sai da ya maimata sannan ta ce masa ta k'oshi.  Ko da suka k'arasa gida falo suka yad'a zango ita da yaran shi kuma ya wuce d'akinsa. Bayan wani lokaci kad'an ya fito ya zauna a falon ya fara yiwa yara wasa har da dariya. Ganin haka ya sa tsam! Ta mik'e ta bar falon ta koma d'akinta. Da kallo ya bita bai ce komai ba. Bayan sun gama zaman ya ce kowa yaje ya kwanta. Dakin sa ya shiga ya kwanta yana ta mazarin yadda zai b'ullo mata saboda ba ya son irin wannan zaman sam. Mik'ewa yayi ya nufi d'akinta, adaidai k'ofar d'akinta ya tsaya sakmakon jin.........

15

Jin sautin muryarta cikin kuka shi ne ya dakatar da shi daga shigar, yana kuma jin yadda take rokon Allah a kansa. Ta na cewa, "Ya Allah wannan zaman na gidann Awwal na gaji da shi, Allah kai ne she da ba ina k'in zaman ba ne don wata mafuta ba, sai dai na tseratar da rayuwata daga fad'awa halaka. Allah ina son Awwa, idan har zai zama irina Allah a sauya shi. Idan kuma ni zan iya zama irin sa to Allah a mai dani. Ya rabb! Idan hakan duka ba za su samu ba Allah ka raba wannan auren domin na tseratar da mutuncina. "  Tana gama fad'ar hakan ta kuma fashewa da kuka . jin irin addu'o'inta sai duka jikin sa ya yi sanyi. A hankali ya bud'e k'ofar d'akinta ya shiga, bai yi magana ba ya je kusa da ita ya zauna.
Kallon ta yayi yaga yadda hawaye suka jik'e mata fuska, tausayi da soyayayyarta duka sai suka lullub'eta. Kafad'ar sa ya jingina da ta ta. Ya ce, "Me kike yi har yanzu baki kwanta ba."
"Sallah nake yi ko ba ka gani ba ne?" Ta bashi amsa cikin kuncin zuciya. Bai ce komai ba yayi shuru yana sauraran fitar lumfashinta. Can kuma sai ya ce, "Ki zo muje d'akina mu kwanta."
"Ba zanje ba Awwal, har sai ranar da ka k'ara k'arfin injin batirin motarka. Domin ba yadda za'ayi a ce kullum idan muka hau ta wuce da kai inda kake son gani amma ni kumata gaza kaini."
Daga haka Samha ta mik'e ta bar wurin bata jira amsar da zai bayar ba. Shi kuwa a zuciyarsa sam kunya ce ta lullub'e shi. Bai san sanda Samha ta falle haka ba har ta ke iya sanar masa wad'annan maganganun. Mik'ewa ya yi bai ce uffan ba ya bar d'akin.
Bayan gari ya waye Samha ta had'a komai ta koma falo ta zauna tana jira ya dawo daga kai yara a makaranta ta tanmbaye shi za ta je gida domin bikin Yaya yusuf ya k'arato kusa. Bai jima ba kuwa ya dawo ya wuceta ya fara cin abincin sa. Ganin haka ya sa ta je inda ya ke ta zauna. Tana zama ya ce, "Ina kwana." Mamaki ya ba ta sosai, domin kullum ita ce take gaidashi ya amsa cikin gadara yau kuma shi ne yake gaisuwar. Amsawa ta yi tare da fad'in, "Ina son ka ba ni dama na je gida,Saboda shirye-shiryen bikin Yaya Yusuf."
Kallon ta yayi sai ta sunkuyar da kanta k'asa.
"Babu damuwa amma ni zan kaiki kuma zan d'auko ki, ba zan so kiyi tuk'i kina cikin damuwa ba."
"Uhm." Shi ne iya abin sa Samha ta furta kawai ta mik'e za ta bar wurin.
"Ina kuma zaki je?" Ya furta cikin k'asa da murya. "Zanje na gama aikina da wuri ne."

"Okay ba damuwa, sai dai baki karya ba kamar."
"Ba na jin yunwa yanzu." Ta fad'a tare da barin wurin don kar ma ya kuma mata wata tambayar. Kitchen ta koma ta fara shirya abincin da za ta tafi da shi gida. Bayan ta kammala komai ta had'a kayan yaranta wanda idan aka kaisu anjima za ta sauya masu.Shiryawa ta yi cikin wata atamfa mai ratsin ja da kuma launin ruwan hanta. Haka jilbab d'in ta ma ruwan hanta ce, takalmi ma haka. Hoda ta sanyawa fuskarta kawai da man leb'e sai turare da ta banbad'a tunda tafiyar daga ita sai mijinta kuma gidansu za ta je. Jilbal d'in ta saka ta d'auko gilashin ta na ido ta fari ta saka. Tana tsaye gaban madubi ya bud'e kofar ya shigo. Kallonta yayi sai dai zuciyarsa ta buga. Ganin irin kyawun da ta yi ga kuma k'amshi me d'adi wanda yake shak'a. Hak'ik'a Samha ta daban ce kuma tabbas ya san yayi dacen mace ta kyakkawa ga ilimin addini ga kuma tsafta ga iya girki. Sai dai matsala guda ta hana su su fuskanci juna. "Ki zo mu tafi idan kin gama. Kuma ki kashe komai ma wutar lantarki."
Da to ta amsa masa ta yi yadda yace d'in. Bayan sun rufe gidan sun shiga mota sun fita suna hanya ya kalle ta tare da fad'in duka wannan turaren da ta saka don zata je gidannan ne? Amsa da ba shi da saboda gidan ne. Shiru yayi bai kuma cewa k'ala ba ganin yadda ta had'e fuska ta juya kai gefe. Har suka isa tukunna ta kalle ahi tare da fad'in. "Za ka shiga ne ko sai ka dawo?" Sai ya dawo ya ba ta amsa. Fita ta yi ta shiga gidan inda ta tarar da su anti dija da maryam duka sun zo su. Farin ciki sai ya mamaye mata fuska amaimakon damuwar da take ciki. Gaida kowa ta yi aka amsa mata sanna ta zauna tare sa ajjiye fulasan hannunta. "Baba ya na ciki ne anti Maryam?" Ta tambaya. Yana ciki suna ba ta amsa. Don haka kai tsaye sai mik'e ta wuce d'akinsa domin gaida shi. Can ta samu Mama da yaya Yusuf suna zaune. Da farin ciki Baba ya dube ta yana fad'in "Mamana ke ce a gidan ?" "Eh wallahi Baba yanzu muka zo. Su ma gaisawa sukayi har da su yaya sannan ta koma wurin si anti Dija. Suma zaune suna hira amma kuma sai suka ga sam hankalinta kamar baya tare da su kamar da ka sancewarta mai surutu. Anti Maryam ta dube ta. " Samha, me yake damun ki ne?"
Jin tambayar ta yi a bazata. Don haka sai ta d'ago kai ta ce..........

16

"Me kiga gani?" "A'a naga sam baki da walwala sosai ne."
Aunty maryam ta ba ni amsa. "Aunty kawai dai ciwon kai nd yake damuna." Carab! Aunty dija take cewa aunty maryam ko dai ciki ne dani. Murmushi kawai na yi domin ba ta san halin da nake ciki bane shi ne kawai. Muna tsaka da zaman mama ta zo tare da kayan akwatin yaya muka fara dubawa. Kaya ne na gani na fad'a masu kyau da tsada. Mama na kalla na ce, "Mama yau she yaya ya kud'ance haka ne? Irin wannan kayan haka, lalle wacce zai aura ta more da kaya masu kyau da tsada."
Murmushi Mama ta yi tare da cewa, "Ai ya jima yana tara kayan sa shi yasa, kuma da yake yanzu yana aiki shi ne yasa siyan na k'arshen aka siya masu tsada."
"Ai kuwa ya kyauta ko ba komai za mu kai kaya ba raini. " murmusawa auntys suka yi suna yaban kyan kayan har muka gama aka maida. Ko da yamma ta yi Yaya ya shigo gida muka masa murna ya sanar damu idan har akwai abin da muka san ana saka wa mu fad'a ya sayo a saka kafin lokacin. Sanar masa muka yi komai ya yi yadda ake buk'ata. Muna tsada da tattaunawar kuwa k'annen mahaifiyar mu suka zo si ganin kayan. Suma ya bawa sukayi aka

maida suka tabbatar komai ya yi. Bamu rabu da su aunty ba har sai bayan magrib sannan suka tafi gidajen su. Ina zaune ina zaman jiran tsammani mama take tambayata ya batun jinnu tana sa ran dai ba na ganin komai yanzu? Amsa mata na yi da komai lafiya yanzu kam sai dai abin da ba za'a rasa ba. Kafin ta kuma magana muka ji Sallamar yaya da Awwal sun shigo, kansa bisa k'asa ya gaida Mamanmu muka fara shirin tafiya gida wansa har su Ameera sun fara shirin bacci da yake ba wutar nefa kuma ba abokan wasan kowa ya tafi da yaransa. Tayar da su duka na yi muka yi sallama da mama. Ya ya ne ya kama hannun yaran ya kaisu mota. Sallama suka yi da Baba da yake k'ofar gida a zaune. Nima sallama na yi masa muka tafi. Muna cikin mota ya dube ni ya ce, "Manyan k'anne biki sai k'aratowa yake. Ni yanzu sati nawa ya rage?" Kauda kai na yi gefe sannan ma amsa masa da cewa, "Sati uku ne."

"Ki ce abin ya zo zamu sha bikin baban yaya ."

"Haka ne kam."

Na bashi amsa.

Daga haka bamu kuma wata magana ba har muka je gida. Koda muka isa na kai yara d'akinsu kowa ya kwanta sai na fito na yi hanyar kitchen domin na dora masa wani abu tunda mu munci abinci shi kuma bai ci ba. Tare ni yayi tare da fad'in "Ba sai kinyi abinci ba, na zo da abin da zan tab'a anjima ki zubamin yana teburin abinci. " Da to na amsa masa na koma d'akina na kunna datar wayata sai kuma na tuna banyi sallar isha ba. Don haka sai na mik'e na je nayi alwala na yi sallah na yi addu'a na kammala. Falo na fito na zauna na kunna kallo na fasa chaty d'in, labarina na kunna a wayata na ajjiye wayar a kan babbar kujera ina kallah kamar tv. Na yi nisa a kallon ina daidai inda maryam takewa mainasara shag'waba a asibiti. Duka sai na ji sun burgen, dama ace ni da Awwal ne haka muke kashe juna da kallon k'auna. Wani murmushi ya yalwatu kan fuskata wanda ban san ina yin sa ba. Ji na yi an d'auke wayar, idanuna na d'ago na kalle shi tare da fad'in lafiya?"

Kallona yayi cikin ido sanna ya d'auke kansa. "Samha wannan da kike kallah fa shirine, karfa kina sakawa ranki damuwa ki b'ata zaman auren ko saboda ganin soyayar film."

"Awwal, daman na tab'a ce maka ina buk'atar soyayyarka? Ko kuwa ka ga ana haska mu'amalar aure anan? Ni fa bana son irin haka ka bani wayata ban shiga sabgar ka ba kaima ban buk'aci ka shiga tawa ba. Tunda ba wani laifi kaga ina aikatawa ba.

" Samha dole na shiga sabgarki tunda ni mijinki ne."

"To maza na san dai maganar ba ta wuce ta abinci ba, muje na zuba maka abin da ka kawo anan aka fi kauri!" Na furta cikin d'aga murya.

"Me kike cewa haka? Kina nufin iya ka cin abinci na iya kenan?"

"Wannan fa kai ta dama ni kazo ka ba ni abin da zan zuba maka kawai."

Bai ce komai ba ya isa wajen firji ya kawo ledoji. Ko da na bude kaji ne masu rai da lafiya gasassu dayar ledar kuma da ya ciro a firjin kayan sanyi ne masu sanyi. Murmushi ne ya kufce min domin Allah ya yi ni da kwad'ayin kaza. Filet na d'auko na zuba masa na ajjiye tawa awani filet d'in na maida guda zan rabawa yara da safe. Zama na na fara ci ba ko jira. Awwal ya gama gane ni sosai, da zarar yaga ina cikin fushi da wannan yake d'auke damuwar. Shiru wurin yayi kowa yana figar kazar sa. Can ya dube ni, "Samha don Allah kiyi hak'uri mu zauna lafiya acikin gidannan kamar na da."

Cak! Na tsaya da cin kazar na ce, "Na hanaka zaman lafiya ne Awwal?"

"Baki hana ba, amma kin san yanzu ina da buk'atar ki a kusa da ni amma kuma kin juya min

baya ."

"Wai saunawa ka juya min baya aba ban ce komai ba sai yanzu dan na raba kaina da wahala shi ne? Sau nawa nake binka ina rok'onka ka saurare ni amma sai dai ka kore ni anyi haka? Awwal a baya rabon ciki ke had'ani da kai kawai kuma na yi hak'uri na zauna, dan yanzu na gaza jurewa shi ne kake ganin laifina? Dan yanzu kazo da yawan bukatar ba biyan bukatar ai awurina duka abu guda ne."

Shuru ya yi kansa a k'asa yana sauk'e lumfashi. Sannan ya ce, "Na ji na d'au laifina kiyi hakuri. Amma yanzu ya kike son na yi Samha."

"Ai ba wani abu bane magani kawai zaka nema ka zauna dani lafiya."

"Samha maganin nan fa duka tallar k'arya ce ba wani abu da zayyi min fa. Da kin ba ni dama na kuma jarrabawa muga yadda za'a yi. ...... "

Tsaye na mik'e na ce, "Dama! Har yanzu wata dama kake nema da zaka cutar dani? To wallahi ba wata dama zan kuma baka har sai ka yi wanka fad'a."

Ina gama fad'ar haka na fashe da kuka mai tsuma zuciya. A mama kance na dago dajin sautin kukan Awwal a gefe na. Yana zaune gefena shi ma yana kuka kamar yadda nake yi. . kallon sa na yi tare da goge fuskata na...........

17

"Kai Kuma mene ne abin kuka?"

Sa ke matse hawayen idanunsa yayi ya ce, "Samha ai dole na yi kuka, ace kullum matata tana kuka saboda ni? Kuma ni na gaza daina saka ta kukan ? Taya zan samu nutsuwa. " "Amma ai kasan hanyar da za ka bi."

"Samha bansani ba! Bansani ba! Ina zan saka kaina wai."

Ita yanzu abin ma mamaki yake ba ta da tsoro, anya kuwa Awwal d'inne ko dai aljanin ne ya dawo. Awwal ne zai tsaya har yana kuka a gabana.

"Samha, wallahi abin yana damuna sosai wallahi, kuma ke kina ganin kamar da gangan nake yi . To yanzu tsakani da Allah mene ne abin yi in ba kukan ba?"

"Cab! nifa wallahi sam ban ma yarda kaine ba, na fi tunanin ko Aljanin ne. " Ta fad'a tana ja da baya. Hannu ya d'aura akan sa tare da, cewa, "Samha, don Allah ki bar wani zancen aljani. Ko wancen ma wani shirina ne kawai amma ba gaskiya ba ne."

Idanu ta zaro waje tana kallon sa tare da fad'in, "Shiri kuma?"

"Samha, muje d'aki na sanar miki."

"D'aki fa ka ce? Ai wallahi dukkan abin da zaka fad'a kawai ka fad'a anan, amma ba inda zanje nikam."

"Haba Samha amatsayinki na me ilimi yanzu ba zaki taimakawa mijinki ba? Ki taimaka ki yi hak'uri ki kuma ba ni wata damar mana."

"Ai Awwal ya kamata ka fahimci ba wata dama yanzu wacce zan kuma baka. idan har baka da abin fad'a anan to ka ga tafiyata."
Tana gama fad'ar haka ta wuce d'aki ta barshi zaune a wurin. iya ka damuwa ya shiga sosai akanta. Kuma ba shi da wani buri da ya wuce ya kasance da ita a wannan dare. Amma ta juya masa baya.
Ita kuwa tana shiga kan gado ta fad'a tare da fashewa da sabon kuka, duniya ta yi mata zafi sam! Ba ta san mene ne abin yi ba a yanzu. wa zata tunkara da wannan lamari ba tare da ta ji kunya ba? Shin ina zata je ta samu nutsuwa a duniya? Da tana da wani wuri da za ta iya fakewa tabbas da ta gudu ta bar Awwal.
Tana tsaka da tunanin sai ta ji wayarta ta yi k'ara bisa ga dukkan alamu sak'on kartakwana ne. Hannu ta mik'a ta janyo wayarta ta fara dubawa, ganin lambarsa ce ya sa ta gane sak'on daga gare shi ya fito. Tana bud'ewa taga ya rubuta, 'Don Allah Samha ki taimakeni kizo ina jiranki.' Tsaki tayi tare da jefa wayar gefen ta. Hannu ta d'aga sama tana fad'in ya Allah ka ga halin da nake ciki da mijina, Allah karka saka ni cikin sahun matan da tsinuwar ka za ta hau kansu. Allah rashin yinsa shi ne zaman lafiyata, yin sa kuwa tamkar jefani cikin mummunan had'arine. Ya ubangijin mu, na kai mak'ura ta yadda ba zan iya jurewa ga kusantuwa ga dukkan wata mu'alar da babu tsuwa cikinta ba. Allah ka kawo mana mafita a zaman aurenmu.
da irin wad'annan addu'o'in har bacci yayi gaba da ita.
shi kansa cikin damuwa ya kwana a wannan ranar.
da safe kuwa ya dubeta ya ce yau za su je gidan hajiya da yamma saboda gobe Mu'azzam zai koma garin su.
da to ta amsa masa tare da jin mugun tausayin sa ganin yadda duk girman izzarsa ta lafa a lokaci guda duka yayi lakwas. lalle ta amince maza ba su kai mata iya jurewa sha'awa ba. yadda ta shiga ta shin hankali a baya ta shan ye aka wuce wurin idan shi ne ya zayyi, ga shi na lokaci guda ma ya gaza!
Abin karyawa ta yi musu suka karya yara kuma aka kaisu makaranta. Don haka sai ta shiga aikin gyran gida domin yau d'aya ta ji sauk'in damuwar da take zuciyarta. bayan ta kammala ta zauna a falo tana chat d k'awayen ta da kuma sister d'inta. ana ma ta samu wani darasi na musamman wanda take jin in sha Allah zuwa dare za ta jarraba Awwal da shi tun da dai neman mafita ake.wuraren Yamma ta gama aikinta ita da yaranta suka shirya cikin kaya na alfarma ya zo ya d'aukesu zuwa gidan hajiya. koda suka je ba k'aramin murna Salma da hajiya suka yi da ganinta ba kasancewar ta d'an kwana biyi bata zo ba.
suna tsaka da gaisawa Mu'azzam ya shigo falon, wata irin kunya duka ta lullib'e Samha domin ba za ta tab'a mantawa da abin da ya faru tsakanin su ba. Kuma ba don tana tsoran Allah babu abin da zai sa ta nunawa Mu'azzam ta gane shi, domin kalar sa shi ne kowacce mace za tayi mafarkin mallaka a duniya. don haka in sha Allah za ta yi iya ka waje ganin Salma ta amshi tayin da yayi domin tabbas ta san za ta yi farin ciki nan gaba.
ganin ta tafi duniyar tunani yasa Salma yi mata magan da cewa "Aunty Yaya yana gaida ke."
Jin ta ambaci kalmar yaya yasa ta yi tunani ko da Awwal take nufi. Don haka sai ta d'aga kanta domin ganin me maganar. gamuwa da idanun Mu'azzam cikin na ta tare da wannan shegen murmushin na shi shi ne yasan ya idanunta sark'ewa cikin nasa............

Ganin idan bata sunkuyar da na ta kanba ba zai dena kallonta ba shi ne yasa ta kalli gefe guda tare da fad'in, "Lafiya lau bakon mu. Ashe tafiya za ka yi gobe kuma."
"Eh wallahi, zan koma garinmu nima na huta da jarabar mijinki kullum cikin gori nake a wurin sa. Don haka ina komawa zan fara shirin aure ni ma."
Duka dariya aka yi masa sanna na ce, "Gaskiya dai kam ya kamata ace ka yi aure ka huta da gorin sa."
Da 'In sha Allah ya amsa min' Muka ci gaba da hira har zuwa dare sannan muka keba da Salma domin tattaunawa. na dubeta na sanar mata cewa matukar tana son Mu'azzam to tayi k'okari ta ba shi dama ayi bikin nan da ita, domin ya cancanta ya zama mijinta kuma yana da duk wani abu da kowacce mace zata so ace mijinta yana da shi. Kallo na ta yi har na kammala zancen sannan ta ce, "Aunty mene ne halayen sa wanda kika sani kuma wasu abu ne wacce mace zata so mijinta ya kasance da su da za ta aura? shi kuma duka yana da su?"
Zama Samha ta gyara tare da fad'in, "Salma, yana da addini kuma yana da ilimin boko da na addini. Sannan ba zaki saka shi cikin munana ba, kuma mutum ne me tsafta, sannan ga barkwanci . Kuma yana da kud'i daidai gwargwado. Sannan yana a matsayin cikakken saurayin da ake saka masa ran me lafiya. Salma Mu'azzam yana k'aunarki, to wanne abu zaki ne ma adukkan wani na miji wanda ba shi ba?  Abu guda ne, Sai dai idan bakya son sa a cikin zuciyar ki. To kinga ana ba wata dabara."
Sunkuyar da kai ta yi bata ce komai ba sannan ta d'ago kai ta dubi Samha ta ce, ""Wallahi ina son sa sosai har cikin zuciyata, sai dai abu guda da nake tunani shi ne. Idan na aure shi dole zan barku ne na bi shi. Ni kuwa ba na son rabuwa da ku. Kuma kin san dole bauci zai kaini."

"Haka ne, amma wannan ba wani abu bane da zai hanaki auren sa ba, domin ba kanki a ka fara auren wani gari ba."
"Haka ne kam aunty, in sha Allah zanyi tunani sosai a kan hakan.

haka dai suka yi ta tattaunawa a tsakanin su har lokacin sallah yayi.

Bayan anyi sallah kowa ya na inda yake basu kuma hallara ba har sai bayan isha. Wanda a lokacin kuma  su Samha suka tattara nasu ina su sukayi bankwana da Mu'azzam suka ta fi.

daga hajiya sai Salma da Hajiya suka rage. Suna ta hira har hajiya ta ce bacci take ji ta tafi ta kwanta.
 ganin haka sai ya zama kamar an basu wata dama ce, matsowa kusa da ita yayi ya sake mata wani murmushi me narkar da zuciya tare da wani sassanyan kallo na soyayya.

sunkuyar da kai ta yi cikin shagwab'a  tare da fad'in " Ya isa haka tom kallon."
"A'a kam, barni na yi ta kallon masoyiyata, domin gobe iwar haka sai dai naga hoto. "

"To yanzu dai goben zaka gudu kenan ka barni?"

"Dole ai, tunda wacce nazo dominta  ba ta sona." Ya bata amsa cikin shagwbe fuska.

"Ya Mu'azzam ni ce bana sonka?"
"To ga Shi kin k'i yarda ki sanar da mama batun amin cewar ki."

"Aa kaima ka san ba zan iya ba, yaya ya kamata ya sanar mata."
"Wow!" Ya furta tare da kaiwa iska naushi. "Yanzu dai kin amince na zama mijinki ke nan?"

"Yaya, idan ban amince ba ya zanyi da k'aunar da nake maka? Ina maka wani irin so wanda ban san ta yadda zan misalta shi ba ."

Baki ya saki yana kallon yadda take furta lafuzzan bakin ta.
haka suka yi ta musayar baitukan soyayya har zuwa kusan sha d'ayan dare. Hakan ta sa shi kusan fita a cikin hayyacin da wanda da kyar ya iya kai kan sa d'aki.

Su kuwa su Samha haka suka ci gaba zama ba wani ci gaba har biki ya zo suka tattara suka koma gidan su domin a yi bikin.
Tafiyarta gida kuwa shi ne silar sake shigarsa damuwa, ganin haka ya ji ya kamata yayi zama ko da wasu daga cikin abokansa domin yaji yadda ake zaman aure don ya gyara kafin Samha ta dawo. Wata k'ila ko akwai wani abu da bai sani ba.
Inuwa abokin sa ya k'ira ya ce su had'u yau da yamma akwai maganar da zasu tattaunawa........

19

A lokacin da Inuwa ya iso gidan baya gida, don haka sai da ya jira zuwan sa tukunna. Ko sa ya iso falo suka yada zango, ruwa da lemo ya d'auko masa tare da cake ya ajjiye masa suka gaisa.
Tambayar sa yayi ya iyalinsa ya tabbatar masa da suna gida sunje biki. bayan dan lokaci da suka d'auka suna hirar duniya sai Awwal yace da Inuwa, "Wai ni kam na tambaye ka mana, a cikin zaman aure me da me mata suka fi so ne."

Dariya Inuwa yayi tare da cewa, "Tofa ka ce madam zata sha gata kenan, lalle kana k'aunarta sosai. A wannan lokacin ina ruwan wasu mazan da abin da matan su suke so."
"Haka ne, amma ina matukar kaunarta, sannan na rasa me zan mata wanda ba zata manta ba. Wannan dalilin yasa na k'iraka don na tambayeka."

Gyara zama Inuwa yayi ya ce, "To Allah ya bar k'auna. A iya sanina da mata gaskiya suna son soyayya, musamman soyayya ta fannin yabawa kwalliya girki da sauran su. Sannan mata suna son kyauta, idan aka ce kyauta to ana nufin ta komai ma.
kuma mata suna son suga ka basu lokacinka ko ta mu'amalar aure ko kuma ta lokacin hira.."

"Okay ma sha Allah da wannan bayanai. Amma naji ka ce lokaci shin akwai wani k'ayyadaddan lokaci da ake bawa mace a lokacin tarayya ko hira ne?"
"A'a ba ina nufin a k'ayyade ba, sai dai lokacin ya zama an maida hankali akan abin da suke da buri. Misali idan mace kuna hira to tana son ka bar komai ka saurareta ko da kuw aikin kasuwanci kake. Haka kuma a lokacin tarayya da kai tana buk'atar dogon lokaci, domin ita mace tafi na miji wasu lokutan rashin gamsuwa da wuri. Amma dai wannna ya danganta da yadda kuka san junanku ne, kawai na baka mislani ne."

Shuru Awwal ya yi domin an zo inda yake so azo d'in.

"Haka ne kam Inuwa, kuma na fahimta.
hira suka ci gaba da yi akan zamantakewar aure da yane shi kansa Inuwa yana da mata har guda biyu. Sai wuraren magrib suka fita a gidan suka wuce masallaci.

Samha ana gida ana didimar biki har ranar auren ta tabbata aka d'aura auren Yaya yusuf lafiya, kowa yana saka albarka da ganin kaya, haka suka d'auka suka kai gidan su amarya aka ba da tukuici suka dawo.
washe gari ma haka suka
Kuma d'aukar wanka kamar su ne amaren ita da yayyunta, kayan maskeru aka kawo masu suma da yamma. kuloli ne da su kafet da shinkafa had'i da samiru dubulan alkaki da abinci da miyar sa da ta ji nama, da dai sauransu.
zuwa dare aka watse kowa ya kama gabansa. Su kuwa sai washe garin ranar sannan suka koma gidajen su.

Tsawon kwana uku da gama bikin ke nan yau.
Samha tana zaune akan d'aya daga cikin kujerun falonta, tana sanye cikin riga da zani ba ko hota a fuskarta kanta ta yi wani kalar d'aurin d'ankwali a har butse, gefe guda kuwa Awwal ne yana zaune ya rasa ta yadda zai fara mata magana ta fahimce shi, saboda yana son su kasance a daren yau amma yana tunanin taya zai mata magana ta saurare shi. Domin a yadda ya ganta ma yau sam kamar bata cikin nitsuwarta.
Jin sallamar aunty Dija shi ne abin da ya sa su waiwaya wa. Zuwa ta yi ta zauna suka gaisa da Awwal sai ya tashi ya fita. Aunty ta dubi Samha ta ce, "Muje ciki."
Bata yi mata musu ba suka shiga ciki abakin gado suka zauna.
Aunty ta dubeta ta ce "Tsarabar da aka fidda miki ce ta biki da na koma gida mama tana neman me kawo wa na ce ta ba ni sai na biya na baki, amma kafinnan Samha me yake damunki? Na jima da fahimtar ba kya cikin nutsuwar ki, kawai ina barin kine bana matsa maki. Yanzu ki dube ki, a gaban mijinki kina zaune ba kwalliya bare wani kyakkawan d'aurin d'ankwali. Shin Samha duk duniya kina da wanda zaki sanarwa da damuwar ki sama da mu ne?"

Shiru Samha tayi ta sunkuyar da kanta k'asa tare matsar hawayen da ya cika acikin idanunta.
"Aunty wallahi ina cikin tashin hankali."
Ta fad'a tare da fashewa da kuka. Rungume ta Aunty ta yi tare da lallashin ta tace , "Karki damu sanar min koma mene ne."

Sunkuyar da kai ta yi k'asa cikin matsananciyar kunya ta ce, "Aunty wallahi injin Awwal ne yana da buk'arar sabis,  kuma kullum na yi ta sanar masa ya k'ara karfin injin amma sam yaki fahimtata.kuma ina tsoran hakan ya jefani cikin halaka. shi ne na yanke shawarar rabuwa da shi amma sam yak'i ya sallame ni."

Jim, aunty ta yi tajin bayanin nata sannna ta yi murmushi ta ce, "Haba Samha, yanzu wannan matsalar akan ta ce zaki ce zaki rabu da uban yaran ki?
na sha mamaki da jin cewa wannan ita ce damuwarki. a tunanina sai dai ko haskawa wasu hanya saboda kasancewar ki wayayya."

"Humm! nayi dukkan abin  da zan iya aunty ina yiwa Awwal.........."
Dukkan k'okarin da Samha tayi ta sanar da aunty sai ta ce da ita, "Samha, kinyi k'okari, amma baki yi abin da ya dace ba har yanzu. kuma kina da laifi kema acikin wasu abubuwan. Don haka yau in sha Allah k'arshen damuwar ki ta zo, zan sanar da ke abubuwa masu mahimmanci wanda baki sani ba na zama da irin wad'annan maza. Sanna kuma zan  sanar dake abin da zakiyi ki samu zaman lafiya da gamsuwar aure a wajen mijinki."
Cike da farin ciki ta gyara zama ta kuma matsowa wurin aunty tare da fad'in, "Ina jinki."

"To Samha, abu na farko dai shi ne.............

*To jama'a laifin dad'i k'arewa, anan na kawo karshen free page na wannan labarin. Don haka ya kamata kununa min asalin soyayya, dalili kuwa ban tab'a sai da muku da littafi ba, kuma ko yanzu da zan sai da ba zan tsawwala muku ba. ganin yadda duniya take cikin wani hali na rashin kud'in kansa. Saboda haka na saka masa kud'i naira d'ari biyu kacal! 200 game bukatar jin cigaban labarinnan ya biya kud'in sa ta wannan lambar akawun d'in. Zara muhammad sunusi first bank
3169199826*

Sai ku tura shedar biyan ta wanna layin da muke magana da ku.

na gode sosai masoya da jimirin bin labari, ina gefe kamad yajin k'osai ina jiran ku.